# Ak'ida a Cikin Darussa Goma

Wallafar

Sayyed Riyadh Al- Hakeem

*Hak'k'in Bugawa Na Mai Mallaka Ne*

*Bugu Na Farko*

*1433 H – 2012 M*

*Cibiyar Al'adun Musulunci Take Yad'awa*


*Ofishin Mai Girma Marja'in Addini Mai*

*Girma Sayyid Hakim (d)*

- **IRAQ** - **Alnajaf alashraf**
  Tel.333180 - 370046 (33 964+) :.
- **IRAN** - **Qum** - P.O.Box 486/37185 :
  Tel - 7740230 (251 98+) :Fax.7742146 (251 98+) :
- **Syria** - **Damascus** - **Sayeda Zaynab (a.s)**
  Tel - 6470752 (11 963+):.Fax.6472058 :
- **Lebanon** - **Beirut**
  Tel - 451634 (1 961+):.Fax.451635 (1 961+) :

Website :http//:www.alhakeem.org
com.alhakeem@info :mail.E

Hakeem, Riyad, 1958-
Ak'ida a Cikin Darussa Goma / Sayyid Riyad Hakeem; Translaiters Munir Muhammad Sa'id, Qum: Darul Hilal, 2010-1431H

ISBN: **978 – 964 – 8276 – 92 – 3** السعر: 10000 ريال

110 ص. مصور . الفهرسة طبق نظام فيپا. المصادر بالهامش.

العنوان الأصلي: العقيدة في عشرة دروس ـ لغة الهوسا (أفريقي)

1. الشيعة ـ اصول الدين ـ المبسط. الف . سيد ، منير محمد، مترجم ـ

عنوان . ج . عنوان: العقيدة في عشرة دروس ـ لغة الهوسا (أفريقي)

**297/41752 Bp 211/5 / 8 ح 704952 ع**

| | |
|---|---|
| *Sunan Littafi:* | *Ak'ida a Cikin Darussa Goma* |
| *Mawallafi* | *Sayyid Riyad Hakim* |
| *Kula Da Tarjama:* | *Munir Muhammad Sa'id* |
| *Sake Dubawa:* | *Hafiz Muhammad Sa'id* |
| *Bugu* | *Na farko* |
| *Mabuga:* | *Fadhil* |
| *Adadi Kwafi:* | *5000* |
| *Tarihin Bugu:* | *1433 H. 2012 M, 1391 H.Sh Mai* |
| *Yad'awa* | *Darul Hilal* |

*ISBN: Lambar Wallafa: 978 – 964 – 8276 – 92 – 3*

بسمه تعالی

*Godiya ta tabbata ga Allah (s.w.t) Kuma Aminci ya k'ara tabbata ga bayinsa wad'anda ya zaba*

***Haqiqa addini a wajen Allah shi ne musulunci.*** *(Suratu Aali Imran: 19)*

*Allah ya shaida cewa; Lalle ne babu abin bautawa sai shi, kuma mala'iku da ma'abota ilimi sun shaida, (ubangiji) yana tsaye da adalci, babu abin bautawa face shi, Mabuwayi, Mai hikima. Lalle ne addini a wurin Allah shi ne musulunci …*(1).

(1) Surar Ali imrana: 18 – 19.

## Gabatarwa

Addinin Musulunci ya xoru a kan kammalallun asasai da hukunce-hukunce, da koyarwa a fagage daban-daban da suka haxa da aqida, fiqihu, tarbiyya, da wasun waxannan. Musamman koyarwar Ahlul-baiti (a.s), waxanda su suke misalta tsarin Musulunci mai asali, tare da la'akari da cewa su suke tare da Kur'ani mai girma. Kamar yadda ya zo a cikin hadisin saqalaini da hadisin jirgin tsira, sai dai siyasar azzaluman mahukunta wanxanda suka riqa al'ummar Musulmi, sun tsananta qiyayya da yaqar Ahlul-Bait (a.s) da qoqarin kawar da karantarwarsu, da tsananta wa Shi'arsu a dukkanin zamunan da suka gabata. Babban misali a wannan zamanin namu shi ne azzalumin shugaban nan wanda ake kira Saddam xan garin Tikrit da jama'arsa, ta yadda suke keta alfarmar mutane da kisan qare dangin da suka dinga yi wa mutane, wanda hakan ya sa sai daga baya aka yi ta gano wasu maqabartu da aka yi ta binne mutane a tskatsakin kudancin Iraqi. Waxannan ayyuka munana da kisan gilla da suke yi wa mutane a wancan lokaci, shi ne muhimman ababen da suka sa a gaba, ba wai yaxa addinin Musulunci ba. Suna ta yaqar ahalin gidan manzon Allah (s.a.w) ta hanyar hana malaman Shi'a rubuce-rubucen Musulunci ta kowace fuska, don

haramta wa al'ummar Musulmi, musamman samari fahimtar ilimin 'ya'yan gidan manzon Allah (s.a.w) da shiriyarsu.

Bayan faxuwar azzalumar gwamnatin Saddam, sai tunanin fara yaxa jerin silsilar koyarwar Musulunci a taqaice don amfanin samari da 'yan mata. Kuma wannan littafin shi ne na farko a kan aqida, wanda na wallafa shi ne a sakamakon wallafa wani littafin da na yi tun a a baya a kan a qida a asirce[1]-a daidai lokacin Saddam ya kai mutuqa wajen kame-kame bisa zalunci Tsawon kwanakin da aka kama ni ya kai tun daga: 25 ga watan Rajab 1403AH, zuwa watan Zulqi'ida 1411 H. Wanda ya yi dai dai da tarihin miladi tun daga 9/4/1983 AD-7/6/1991 AD.

A taqaice dai na wallafa wancan littafin a cikin kurkuku sakamakon roqon da wasu `yan'uwa daga cikin samarin muminai suka yi waxanda muke tare da su a cikin kurkukun –wanda yake qarqashin kurkukun **Abu Guraib** wanda ya kai nisan km 35, daga yammacin Bagdad, kuma mun sami damar yawaita shi da kuma aika shi zuwa xakunan ‘yan kurkukun da kuma koyar da su shi.

Sai dai tuni aka vatar da irin wancan littafin ta hanyar sa qarfi da tilastawa, sakamakon

(1) Amma yadda aka yi na sami kayan rubutu da sauran su shi ma yanada tasa qissar na fayyace ta a labarin kamu.

mummunan kawo hari na kutse da binciken da mahukuntan wancan lokacin na neman kowane irin littafi da yake xauke da koyarwar 'ya'yan gidan Annabi Muhammad (s.a.w), ko da kuwa wasu 'yan takardu da makamantasu aka samu, ballantana kuma littafin Aqida da wani daga cikin 'ya'yan Hakim ya rubuta don kada ya ba da damar dawowar matsayin wannan gida na zuriyar Hakim. Wanda wannan zai zama sababin kashe mutane da yawa, musamman samari sakamakon aiwatar da dokar nan ta azzaluman mahukuntan zamani Saddam (L), wacce ke cewa:- Duk wanda aka same shi yana rubuce-rubuce a kan wayar da kan al'umma a kan abin da ya shafi addininsu da rayuwarsu da kuma nishaxantar da su a cikin kurkuku, to hukuncinsa shi ne kisa, kuma da man kisa ne sakamakon da ya fi kusa-kusa ga duk wanda hukumar ba ta son sa.

To amma a kowane hali, bayan faxuwar waccan muguwar gwamnati da ta yi xare-xare a kan qirjin Iraqi da Iraqawa, sai ya zama dole mu yi amfani da wannan damar domin mu sanar da 'ya'yanmu masu tasowa tushe da asalin aqidunsu ta hanya mai sauqi. A matsayin taqi na farko domin yaxa koyarwar musulumci ta asali a cikin al’ummar mususlmi da izinin Allah maxaukaki, ina mai roqon Allah maxaukaki da ya sanya shi karvavve kuma tsarkakke a gunsa mai girma, kuma mai

amfanarwa ga masoya matasa maza da mata. Allah maxaukaki ya datar da mu zuwa daidai!

Hujjatul Islam Sayyid Riyad Al-Hakim

1424 H

# Ginshiqan Addini Guda Biyar Ne

**1- Tauhidi**
**2- Adalci**
**3- Annabci**
**4- Imamanci**
**5- Alqiyama**

## Darasi Na Xaya

## Ginshiqan Addinin Musulunci

## Ginshiqi na Farko: Kaxaita Allah

Abin da ake nufi, shi ne tabbatar da samuwar Allah (s.w.t), wanda ya halicci wannan duniyar, kuma shi kaxai ne ba shi da abokin tarayya. To a nan zamu kasa darasin zuwa kaso biyu, kamar haka:

1- Na xaya, shi ne tabbatar da Allah (s.w.t) mahaliccin duniya, domin ba ita ta samar da kanta ba tare da mahalicci ba. Akwai dalilai da yawa da suke tabbatar da cewa duniya ba ita ta samar da kanta ba, za mu kawo wasu daga ciki.

**Dalili Na Farko:** Shi ne cewa dukkanin wani abu samamme a wannan duniyar yana iya qarewa a rasa shi, kamar yadda muka ga abubuwa da yawa sun qare kuma muka rasa su a yanzu, wanda yake nuna samuwarsu ta dogara ne da waninsu, ba daga asalin zatinsu samuwarsu ta faru ba, domin da haka ne da ba zai yiwu su qare ba. Tun da kuwa zama suna iya zama babu, lallai ba makawa wanda ya samar da su, shi ne Allah (s.w.t) wanda har abada ba zai qare ba.

Bari mu ba da misali don faxaxa tunani: Mu qaddara cewa akwai wasu madubai ko gilasai da suke xauko haske daga wani waje zuwa wani waje, misali gilashi na farko ya xauko haske ya haska wa na kusa da shi, shi ma ya haska wa na kusa da shi, haka nan har zuwa qarshen duniya. Yayin da mutum ya ga wannan hasken da yake fitowa daga madubai, zai fahimci cewa kowane xaya daga cikin gilasan nan ba shi ne ya mallaki wannan hasken ba, domin a bisa xabi'ar gilashi shi kansa ba shi da haske, sai dai ana iya amfani da shi domin ciro haske daga wani wuri zuwa wani wurin. Shi ya sa xan Adam ba zai yi tunanin ya yi bincike a kan hasken da yake tsakanin gilashi da gilashi ba, sai dai mutum yana yin binciken ne a kan abin da yake wajen gilasan, kamar rana ko fitila.

Kamar yadda hasken nan dole ne ya koma zuwa ga mafarin da zai zama shi ne asalinsa, ba wani abu daban ba. Haka nan lamari samuwa yake, babu makawa sai (samamme) ya dogara da wani wanda shi yake ba shi samuwa, wanda haqiqa ba ya rasa samuwa a kowane lokaci, wanda kuma shi ne Allah (s.w.t).

**Dalili Na Biyu:** A taqaice: Wannan duniya wacce take cike da kyakkyawan tsari, ta yadda kowane vangare nata ya dace da xaya vangaren, ko kuma duk vangarorinta sun dace da juna, saboda ci gaban ilimi a kullun ana iya gano sababbin abubuwa na mamaki da suke tabbatar da kyawun tsarinta. Lallai babu makawa wanda ya halicce ta ubangiji ne mai ilimi da hikima, hankali ma ba zai yarda ba ne a ce wai duniya da kanta ta samar da kanta, ko kuma a fassara ta da cewa ta samu ne sabo da wasu abubuwa masu sauqi da suka faru, waxanda za a iya ganin su ko a ta'allaqa su ko suke xamfare da ita ba. Shin akwai wani mai hankali da zai shiga cikin gidan da aka tsara kayansa suka tsaru suka yi kyau, duk da kasantuwar kayan kala-kala ne, sannan ya ce kai amma gidan nan ya tsara kansa da kansa? To idan har hankali ba zai yarda da haka ba, ta yaya zai yarda da cewa wannan tsarin da muke gani a wannan duniya mai abubuwan mamaki wai shi ya samar da kan sa, ba tare sa wani mahallici masani mai hikima da ya samar da ita ba?!

Allah (s.w.t) yana cewa: "Da sannu za mu nuna musu ayoyinmu a dukkanin sassan duniya, kai har kawukansu, har sai ya bayyana a gare su cewa al'amarin Allah gaskiya ne. Shin bai isar wa ubangijinka abin alfahari ba cewa, shi mai shaidawa (masani ko mahalarci) ne a kan komai ba". (Suratu Fussilat:53).

## Darasi Na Biyu

### Mahaliccin Duniya

Mahaliccin Duniya Shi Ne Allah (s.w.t) Wanda Ba Shi Da Abokin Tarayya: Dalili a kan haka shi ne cewa, da a ce akwai alloli da yawa, kuma kowane Allah ya wadatu da barin wani, to da manufofin waxannan allolin sun ci karo da juna da lalacewar tsari, da wargajewar sama da qasa, kamar yadda Allah (s.w.t) yake faxa a littafinsa mai tsarki: **Da ya kasance tsakanin sama da qasa akwai Alloli da sun lalace**. (Suratul Ambiya:22).

Kai daga cikin abin da yake qara tabbatar mana da cewa Allah xaya ne, shi ne ba mu tava ganin wani Annabin da aka aiko daga wajen wani Ubangiji daban ba Shi maxaukaki ba.

**Ginshiqi Na Biyu: Adalci**

Ma'anarsa shi ne Allah (s.w.t) adali ne, ba zai yiwu ya yi zalunci ko kuma ya zalunci wani ba, domin adalci siffa ce ta alheri, zalunci kuwa siffa ce ta sharri, babu wanda yake fakewa zuwa zalunci sai dai masharranci ko mai raunin da ya kasa tabbatar da hadafinsa ko buqatunsa ta hanyar adalci. Amma Allah (s.w.t) shi ne mavuvvugar dukkanin alheri kuma shi yake ba wa dukkanin halittunsa samuwa, kuma ya wadata daga barinsu, saboda Allah (s.w.t) ba ya buqatuwa zuwa yin zalunci kamar yadda ya faxa a cikin Kur'ani mai girma: Ya ku mutane ku ne mabuqata zuwa ga Allah shi kuwa mawadaci ne abin godiya. (Suratu faxir: 15).

A wata ayar kuma yana cewa: **Haqiqa Allah ba ya zalunci ko da kwatankwacin qwayar zarra, idan ayyukanku suka kasance masu kyau zai nunka muku ya kuma ba ku lada mai girma daga gare shi**. (Suratun nisa'i: 40).

Qari a kan adalci, Allah (s.w.t), ya siffanta da cikakkiyar kamala ta kowace fuska, domin shi rayayye ne mai qarfin iko a kan kowane abu, mai ilimi da hikima, shi ya halicci halitta, shi yake shimfaxa arziqi kuma shi mai tausayi ne, mai rahama da sauran siffofi na kamala, Sannan ya tsarkaka daga dukkanin tawaya da rauni.

**Ginshiqi Na Uku: Annabta**

Haqiqa Allah (s.w.t) bai halicci duniya don wasa ba, kamar yadda ya faxa a cikin Kur'ani mai girma: **"Ba mu halicci sammai da qassai da abin da ke tsakaninsu domin wasa ba. Ba mu halicce su ba sai don gaksiya, sai dai mafi yawan mutane ba su sani ba"**. (Suratu dukkhan:38-39).

Haqiqa Allah (s.w.t) ya sanya wannan duniya ta zama gada ga xan Adam zuwa lahira, kuma ta hanyar ayyukansa da dacewarsa a wannan duniyar zai sami sakamako da darajarsa a lahira. Saboda haka Allah (s.w.t) ya shiryar da mutum tafarki madaidaici, ya kuma fuskantar da shi zuwa ga alheri ta hanyar wasu salihan bayi masu ikon xaukar nauye-nauye da saqon ubangiji ga al'umma, irin waxannan mutane su ake kira (ANNABAWA).

Annabi shi ne yake xauke da saqon ubangiji Allah, da kuma koyar da al'umma, waxannan ana kiransu (ARRUSUL).

Haqiqa Allah (s.w.t) ya aiko Annabawa da yawa a zamunan da suka gabata, daga cikinsu akwai:

1- Annabi Nuhu (a.s).

2- Annabi Ibrahim (a.s).

3- Annabi Musa xan Imrana (a.s) shi ne wanda ya zo da addinin Yahuwa. An sauko masa da Attaura.

4- Annabi Isa xan Maryam (a.s) wanda ya zo da addinin ciristanci, kuma aka saukar masa da Injila.

Annabi Muhammad (s.a.w), xan Abdullahi xan Abdul Muxallabi, wanda ya zo da addinin muuslunci. An saukar masa da Kur'ani mai girma, babu wani Annabi a bayansa, kuma shi ne qarshen annabawa da mursalai. Duk wanda ya yi da'awar annabta a bayansa to wannan maqaryaci ne.

Kamar yadda Allah maxaukaki ya faxa: **Muhammad bai kasance uban xaya daga cikin mazajenku ba, kaxai shi manzon Allah ne, kuma cikamakin annabawa**.

Ana kiran waxannan annabawa guda biyar: **Ulul azmi**, wato (mafiya xaukakar annabawa).

## Darasi Na Uku

### Siffofin Annabi (s.a.w)

Kasantuwar Annabi shi ne yake xauke da saqon Allah (s.w.t), babu makawa sai ya kasance wanda zai iya xaukar wannan nauyin, kuma ya zama ya cika waxannan siffofi masu zuwa:

1- Jarumtaka, ya zama ba ya jin tsoron azzalumai, kuma ba ya karaya ko gazawa ko yin rauni a sakamakon barazanarsu da cutarwarsu.

2- Gaskiya, domin yana xauke ne da saqon Allah, babu makawa sai ya kasance mai gaskiya, dominmaqaryaci bai cancanci ya xauki saqonsa ba, saboda mutane ba za su gasganta shi ba.

3- Amana, shi mai isar da saqon Allah ne cikakke, ba tare da canji ba ko kuma jirkirawa, kuma ba zai ha'inci ubangijinsa ba.

Haqiqa an san Annabi (s.a.w) da kyawawan xabi'u, musamman gaskiya da riqon amana tun kafin a aiko shi, har ma mutanen Makka suna yi masa laqabi da mai gaskiya, mai amana, suna kuma ba shi kayansu amana. A lokacin da manzon Allah (s.a.w) zai yi hijira a voye daga Makka zuwa Madina, sai ya yi wa Imam Ali (a.s) wasiyya da ya kwanta a kan shimfixarsa, domin kada mutanen Makka su san ya yi hijira. Kuma

domin Imam Ali (a.s) ya mayar wa mutane amanarsu da suka ba wa manzon Allah (s.a.w), kuma Imam Ali (a.s) ya aikata hakan.

4- Tabbatuwa a kan aiki da biyayya ga Allah (s.w.t), ta yadda mutane za su yi koyi da shi, su rinqa bin umarninsa da abin da ya nuna musu domin idan Annabi ya sava wa Allah (s.w.t), kenan ya qarfafi mutane a kan savonsa.

Saboda haka ake cewa wajibi ne annabawa su zama ma'asumai. Isma wata aba ce da take mallakakkiya kuma tabbatacciya a cikin zuciya, kuma baiwa ce ga mutum da yake samun tabbatuwa da ita, ya kuma nisanci savon Allah (s.w.t).

Haqiqa Annabi ya tattara dukkanin kyawawan xabi'u da haquri da sauransu.

Yana daga abin da aka ruwaito na daga haqurinsa (s.a.w) a yaqin Uhudu, yayin da aka karya masa haqori, aka ji masa rauni a girar idanunsa! Sai wani daga cikin sahabbansa ya ce: Me zai hana ka yi addu'a a gare su, sai Allah ya amsa. Sai manzon Allah ya ce: **"Ai ni ba a aiko ni in zama mai tsinuwa ba, an aiko ni ne domin**

**na zama mai kira ga rahma. Ya Allah ka shiryi mutanen nan, domin su ba su san ni ba".** [1]

(1) Mu'ujamul Kabir:11/189.

## Mu'ujiza

Kasantuwar annabawa su ne masu isar da saqon Allah (s.w.t) da koyarwarsa, sai ya zama dole ne a gwama da'awarsu ta annabata da abin da zai tabbatar da gaskiyarsu da alaqarsu da Allah (s.w.t), ta hanyar mu'ujiza wacce take qarfafa da'awar tasu.

Mu'ujiza ita ce wani abu da zai faru domin tabbatar da gaskiyar Annabi, ya kuma sava wa xabi'ar xan Adam kuma ya zama ba irin na yau da gobe ba.

Ba don gwama mu'ujiza da da'awar annabawa ba, da tantance tsakanin annabawa da Allah (s.w.t) ya aiko da kuma maqaryata masu rufa-ido ba zai zama mai sauqi ba wanxanda suke da'awar annabata ta qarya, kamar Musailamatul kazzab, da Al'aswadul Ansi da wasunsu daga cikinm manyan shaixanun kowane zamani.

## Misalan Mu'ujizozin Annabawa

1-An yi wani azzalumin sarki a lokacin Annabin Allah Ibrahim (s.a), wanda yake mai xagawa kuma mai tsananin kafirci ana kiransa da suna Namarudu. A lokacin da ya ji kiran da Annabi Ibrahim yake yin a a bauta wa Allah (s.w.t) shi

kaxai, sai ya kira shi ya tattauna da shi a kan ikon Allah (s.w.t), sai Annabi Ibrahim (a.s) ya ce masa: Ai Allah (s.w.t) shi yake kashewa kuma shi ne yake rayawa. Sai Namarudu ya ce: Ai ni ma ina kashewa kuma ina rayawa, ma'anarsa shi ne duk wanda na yanke masa hukuncin kisa, sai in yafe masa, ke nan na raya shi, mutumin da yake raye kuwa sai in kashe shi.

Sai Annabi Ibrahim (a.s) ya ce, cikin abin da Kur'ani ya zo da shi cewa: **"Allah (s.w.t) shi ya ke fito da rana daga Gabas, saboda haka, kai kuma ka zo da taka daga yamma, Sai kafirin ya kunyata".** Suratul Baqarati: 258.

Yayin da (Namarudu) ya ga ya gaza yin jayayya da Annabi Ibrahim, bisa hujja sai ya ximauce sannan ya xauki mummunan mataki na kisa a kan Annabi Ibrahim (a.s) (kamar yadda yake dama shi ne al'adar azzalumin da ya kashe kare kansa da dalilai a lokacin tattaunawa). Sai ya xauki matakin qona shi da wuta, domin ya tsoratar da mutane kada su yi imani da Allah (s.w.t). Ya saaka tara itace mai yawa, aka kunna wuta, aka jefa Annabi ibrahim a tsakiyarta, sai dai Allah (s.w.t) ya tseratar da Annabinsa Ibrahim (a.s) daga wutar namarudu, ya kuma sanya wutar ga Annabi Ibrahim (a.s) kamar yadda Allah ya faxa a cikin Kur'ani mai girma:

**"Sai muka ce: Ya ke wuta ki kasance sanyi da aminci ga Annabi Ibrahim". Suratul Ambiya:69.**

Sai ya zama tseratar da Annabi brahim daga wannan gagarumar wuta mu'ujiza ce a gare shi, kuma dalili ne a kan annabtarsa (a.s).

2 – Yayin da Allah (s.w.t) ya aiko Annabinsa Musa (a.s) zuwa ga Fir'auna da mutanensa, domin ya kira su zuwa ga bautar Allah shi kaxai da imani da saqonsa, sai ya haxa masa da mu'ujizozi. Daga cikin muhimmansu: Akwai sandar Musa, ta yadda idan ya yarda da ita a qasa sai ta zama macijiya, mai firgita yan kalloi. Amma Fir'auna sai yake zaton yin hakan sihirin Musa ne ba mu'ujiza ce daga ubangijin talikai ba. Sai ya tara dukan matsafan zamaninsa ya kuma umarce su su yi tsafi da rufa-ido. Suka zo suka sihirce mutane, ta yadda idan suka jefar da sandunansu da igiyoyinsu sai su zama kamar macizai, Amma da Annabi Musa (a.s) ya jefa sandarsa, sai ta zama babbar macijiya mai girma, duk ta haxiye sandunansu da igiyoyinsu. Yayin da matsafan suka ga haka,sai suka fahimci cewa abin da Annabi Musa ya yi ba tsafi ba ne, mu'ujiza ce daga Allah (s.w.t), gaba xayansu suka yi imani da Allah (s.w.t).

Kamar yadda Kur'ani mai girma ya kawo: **Yayin da matsafan suka zo, sai suka ce wa fir'auna: Shin muna da sakamako na musamman idan**

**muka yi nasara? Sai ya ce qwarai. Kuma lalle za ku kasance daga cikin makusanta. Sai Annabi Musa (a.s) ya ce musu: Ku jefa abin da za ku jefa. Sai suka jefa sandunansu da igiyoyinsu, suka kuma ce: Mun rantse da buwayar fir'auna, lallai mu za mu yi galaba. Daga nan sai Annabi Musa (a.s) ya jefa sandarsa, sai ta haxiye duk abin da suka jefa a nan. Matsafan suka faxi suna masu sujjada, suna cewa: Mun yi imani da ubangijin talikai.** Suratus shu'ara:41-47

Sai Sandar Musa (a.s) ta kasance mafi girman mu'ujizar da take tabbatar da annabtarsa.

3– Haka nan lokacin daAllah (s.w.t) ya turo Annabi Isa xam Maryam (a.s) a matsayin Annabi, ya kuma saukar masa da Injila, mu'ujizarsa ta kasance warkar da cututtuka masu wahalar warkewa, kamar makanta da kuturta. Kuturta ita cecutar fata da take sa fata ta bushe ta yi fari, da kuma raya matattu. Ya kuma suranta wata dabba da tavo, sannan ya yi busa a cikinta, sai ta zama dabba (rayaiyiya). Ya kuma bas u labarin abin da suka aikata a gidajensu, amma dukkanin waxannan ya yi su ne da izinin Allah (s.w.t).

kamar yadda Allah (s.w.t) ya faxa a cikin Kur'ani mai girma: **"Kuma manzo ne zuwa ga Bani isra'il, lalle na zo muku da ayoyi daga wajen ubangijinku, lalle ni zan iya halitta**

**muku tsuntsu daga tavo, sannan kuma na yi busa a cikinsa sai ya zama tsuntsu da izinin Allah. Sannan na warkar da makaho da kuturu, na kuma raya matacce da izinin Allah. Kana na ba ku labarin abin da kuka ci, da abin da kuka voye a gidajenku. Haqiqa a cikin wannan al'amarin akwai faxakarwa gareku idan kun kasance masu imani".** Suratu Aali Imrana:49.



Hoton kabarin manzon Allah a cikin masallacin Madina abar haskakawa.

## Darasi Na Huxu

## Mu'ujizar Annabi (s.a.w)

Da'awar Manzon Allah (s.a.w) tana tare da mu'ujizozi da yawa, za mu kawo waxansu da yawa:

1. Bayan manzon Allah (s.a.w) ya fara kiran mutane zuwa ga musulunci, mushirikai suka ga yadda Allah ya xaga shi da sahabbansa a kan yaxa addinin Musulunci da kira zuwa kaxaita Allah shi kaxai, da kuma yin watsi da shirka da bautar gumaka, sai mushirkan suka fara cutar da su da azabobi kala-kala, tare da yin barazana ga manzon

Allah da sahabbansa. Kai har suka yanke shawarar sanya musu takunkumin tattalin arziqi da hana jama'a su yi mu'amala da su, musamman shi Annabi Muhammad (s.a.w) da sahabbansa da qanin mahaifinsa abu talibi da danginsa Banu hashin da Banu Abdul Muxallabi, tare da kuma tsare su a wani kango da ake kira lungun Banu Hashim, bayan shekaru shida da aiko manzon Allah (s.a.w).

Quraishawa sun yi alqawari a tsakaninsu, suka kuma rubuta shi a tsakaninsu, na zalunci a kan cewa kada a sayar musu da kaya, kuma kada a saya daga gare su, kada a aurar musu kuma kada a aura daga gare su, kada kuma a yi dukkanin wata mu'amala da su har sai sun bayar da Muhammad an kashe shi. Sannan muka buga tambari har guda takwas a jikin takardar, Mansur xan Ikiramata shi ne ya rubuta takardar, yana gama rubutawa hannunsa ya shanye. Sai suka rataye ta a jikin Ka'aba a watan Muharram, shekarata ta bakwai (7) bayan hijira. An tsare su tsawon shekara uku (3). Manzon Allah (s.a.w) ya sha wahala da Banu Hashim tare da sauran sahabbai wahala mai tsanani. A nan manzo (s.a.w) da Abu Xalib da Khadijatu 'yar Huwailid suka yi ta ciyar da dukiyoyinsu. Sun kasance suna sayo kaya a voye da farashi mai tsada, kai har dai wahalar ta yi musu yawa.

Sai (Mala'ika) Jibiril ya zo wajen manzo (s.a.w), ya ba shi labarin cewa, Allah (s.w.t) ya aiko da gara ta cinye takarda sai wurin daka rubuta sunan Allah (s.w.t) kawai za ta bari. Manzon Allah (s.a.w) ya ba wa qanin mahaifinsa wannan labari.

Sai Abu Xalib ya tara Quraishawa ya qalubalance su yana mai cewa: Ya ku mutane ku kawo takardar taku, ta iya yiwuwa mu sami mafita da kuma hanyar sadar da zumuncinmu da barin wannan takunkumi. Sai suka kawo ta da kuma tambarinsu a ciki. Sai ya ce ita ce takardar da kuma rubutun alqawari a cikin ta kuwa? Babu musu suka ce ita ce. Sai ya ce shin kun yi wani abu a cikinta? Sai suka ce: A'a.

Sai ya ce: To Annabi Muhammad (s.a.w) ya sanar da ni daga ubangijinsa cewa, Allah (s.w.t) ya aiko da gara ta cinye duk abin da yake ciki sai dai ambaton Allah (s.w.t) shi kaxai ne ba ta cinye ba. Shin ya ya za ku idan abin da ya faxa ya tabbata gaskiya ne? Sai suka ce za mu yarda, mu warware wannan alqawarin.

Sai ya sake cewa: Idan kuma qarya ya yi, to ni zan ba mu shi ku kashe shi. Sai suka ce: Lallai ka yi adalci kuma ka kyautata. To daga nan sai aka buxa takardar, kawai sai su kaga, ga ara ta cinye komai, sai dai wajen da aka rubuta 'da sunan Allah mai xaukaka da buwaya', amma mutanen naka sai suka ce ai shihiri ne. A wannan ranar

mutane da yawa suka musulunta. A wannan lokacin mutanen duka suka fito, har da Banu Hashim da Banu Abdul Muxallabi duka suka fita, ba su sake komawa ba.[1]

Wannan mu'ujiza ta kasance dalilin musuluntar waxannan mutanen.

2. Yayin da manzon Allah (s.a.w) ya yi hijira tare da ABubakar a voye, daga Makka zuwa Madina. Sai Quraishawa suka aika mutane da yawa a kan dawakai domin su kamo manzon Allah (s.a.w), su dawo da shi garin Makka ya wanzu a qarqashin ikonsu. Sai manzo Allah (s.a.w) da Abubakar suka shiga cikin kogon hira, sai quraishawa suka hau kan kogon domen su binciko shi, sai Allah (s.w.t) ya sa giza-gizo ya rufe wajen da yanarsa, kuma tsuntsuwa ta zo ta yi sheqa a kai, ta kuma zauna. Su kuma arna suka zo suna ta binciken inda Annabi yake a cikin kogon.

Yayin da waxannan arna suka yanar gizo-gizo da kuma sheqar tsuntsu a kai, sai suka yi zaton ba zai yiwu a sami mutum a cikin wannan kogo ba.

Haka nan waxannan mahaya dawakan suka dawo suna masu baqin cikin kuma tavavvu.

Sai dai, wani mugu (xan ta kife) da ake kira Suraqatu xan Jash'umi ya fita daga Makka don

(1) Tarihin ya'aqubi: j1/32.

neman manzon Allah (s.a.w), saboda kwaxayin kuxin da aka ce za a bayar ga duk wanda ya kamo manzon Allah (s.a.w) na raquma xari (100) duka sa ga duk wanda ya kamo manzon Allah (s.a.w), musamman a tsakanin Makka da Madina, domin tafiya ce mai tsawo sama da kilo mita xari huxu (400 km).

Bayan manzon Allah (s.a.w) ya fito daga kogon Hira, ya ci gaba da tafiya zuwa Madina shi da Abubakar, sun kusa zuwa Madina, sai ga Suraqatu ya zare takobinsa. Sai manzon Allah (s.a.w) ya ce: Allah ka kare ni daga sharrin Suraqatu da duk abin da ka so. Sai qasa ta kama qafar dokinsa, Suraqatu ya ce: Ya Muhammad, na san saboda kai qasa ta kama qafar dokina, ka roqa mini Allah ya saki dokin. Na rsantse da rayuwata, idan har alheri bai same ku ba daga gare ni to sharri ba zai same ku ba daga gare ni.

Sai manzon Allah (s.a.w) ya yi addu'a, Allah (s.w.t) ya saki dokin, amma arnen bai haqura ba. Har sai da ya maimaita kai wa manzon Allah (s.a.w) hari har sau uku, shi kuwa manzo yana roqa masa Allah qasa ta saki dokinsa.

Lokacin da ya dawo Makka ba tare da ya iya kamo Annabi ba, ya ba su labarin abin da ya faru sai suka qaryata shi, wanda kuma ya fi qaryata shi shi ne Abu jahil. Suraqatu ya yi wasu baituka kamar haka:

Ya baban hikima, wallahi da a ce ka ga,

Al'amarin dokina, lokacin da qasa ta kama shi,

Da ka fahimta, kuma ba ka qara shakku ba a kan cewa Muhammad,

Manzo ne, kuma hujja ne. (1)

Waxanan abubuwa da suka faru guda biyu, a yayin tafiyarsa hijira na shigarsa kogo da kuma kamun da qasa ta yi wa dukin Suraqatu) dalili ne a kan annabtarsa.

Manzon Allah (s.a.w) ya kasance yana da mu'ujiza dawwamammiya wacce ta fi duk waxannan, ita ce mu'ujizar Kur'ani mai girma.

(1)Wannan nassin an ciro shi ne daga usulul kafi 8/263, da kuma tarihil Yaqubi 2/40.

## Darasi Na Biyar

### Kur'ani Mu'ujiza Madawwami

Tun da manzon Allah (s.a.w) ya kasance shi ne cikamakin annabawa da mursalai, kuma saqon musulunci shi ne cikamakin saqon Allah maxaukaki, sai ya zama dole mu'ujizarsa ta zama dawwamammiya, da dawwamar addinin Musulunci. Wannan mu'ujiza kuwa ita ce Kur'ani mai girma, wanda ya kasance kogi ne ga malamai da masu fasaha bisa dukkanin abin da ya qunsa, da kuma irin karantarwarsa, ga shi kuma tabbatacce tun daga lokacin manzo har qarshen duniya.

### Za Mu Kawo Wani Vangare Na Kalubalen Kur'ani Mai Girma

1 – Qalubalensa Ga Masu Taqama Da Balaga Da Fasaha Na Zamaninsa:- Kur'ani ya zo da balaga da fasahar da Larabawan wannan zamanin masana balaga da fasaha suka kasa jayayya da shi, duk da qalubalen da ya yi musu da kuma qarancin musulmai a wancan lokacin a Makka. Ga qalubalen: **Ka faxa musu cewa, da mutum da aljan za su haxu a kan su zo da misalin wannan Kur'anin ba za su iya ba, ko da kuwa sashinsu zai taimaka wa sashi**. Suratul Isra'i:88.

Wani qalubalenn da ya fi wannan sauqi shi ne, su zo da ayoyi goma kacal amma suka kasa: **"Shin ko suna cewa: Qirqiro shi ya yi!?, to faxa musu su qirqiro ayoyi goma irinsa, su kuma kira abin da za su iya ba Allah ba, idan sun kasance masu gaskiya. Idan ba su iya amsa muku ba, to ku sani cewa, duk abin da aka saukar to da ilimin Allah ya sauka**. *Suratul Huud:13-14.*

Qalubale na qarshe da Kur'ani ya yi musu shi ne: Tun da sun kasa kawo waxancan, to su zo da sura xaya kacal, in da Allah (s.w.t) yake cewa: **"Idan kun kasance masu shakku a kan abin da muka saukar wa bawanmu, to ku zo da misalin sura xaya irinsa, sannan ku kira shaidunku ba Allah ba, idan kun kasance masu gaskiya. Idan kuwa ba ku iya ba, to ba za ku iya ba har abada, kana ku ji tsoron wutar da makamashinta shi ne mutum da duwatsu, an kuma tanade ta ne saboda kafirai**. Suratul Baqarati: 23-24.

Idan muka yi la'akari da wannan qalubalen da Kur'ani ya yi wa Mutane da Aljanu musu ba kawai ya taqaita da lokacin manzon Allah ba ne, domin ya tattara dukkanin zamunan da mutum da aljan suka rayu. Da a ce mushirikan nan za su iya karvar waxannan qalubalen to da sun zo da misalin Kur'ani, ko ayoyi goma ko kuma sura

guda xaya. Duk da cewa Larabawa a wancan lokacin sun kasance masana balaga da fasaha, musamman larabawan maka, a lokacin da manzon Allah (s.a.w) da musulmi suka kasance 'yan kaxan masu rauni.

Muhirikai kuwa sun kasance cikin damuwa da tashin hankali a kan abin da manzon Allah (s.a.w) ya sa a gaba, da kuma dagewarsa a kan yaxa addinin Musulunci, da kuma jureriyar sahabbansa akan dukkaninnau'o'i na azaba da suke yi musu, don tsoron yaxuwa wannan sabon addinin. Domin a sakamakon haka, mushirikan za su kai ga rasa matsayin da suke da shi a jazirar Larabawa. Saboda haka! Da a ce za su iya gogayya da Kur'ani da sun karvi qalubalen da Kur'ani ya yi musu, da kuma sun kaucewa fuskantar manzon Allah (s.a.w) da sahabbansa, da yaqi da shan kashi a fagen fama, da kuma rayukan da suka qaddamar saboda hakan.

Haqiqa masu tarihi sun ruwaito halayen ruxewa da yawa na manya-manyan mushirikai da gamsuwa da yadda Kur'ani ya yi fata-fata da su, da kuma ximaucewarsu wajen kasa yi masa hukunci ko matsaya ta musamman. An kuma ruwaito daga Walind xan Mugira Almakhzumi, wanda ya kasance shugaba na mawaqa da adabi a wannan lokaci, yayin da ya ji wasu ayoyi daga Kur'ani mai girma sai ya ce: "Wallahi na ji wata

magana daga Muhammad ba ta yi kama da maganar mutane ba ko aljan, haqiqa maganar tana da zaqi kuma tana da ado. Kai! A saman maganar akwai kayan marmari ('ya'yan itatuwa), a qasan ta kuwa akwai ruwa mai daxi -abin sha mai daxi-, kuma magana ce mafificiya, babu wata magana samanta"[(1)].

Yana daga cikin abu mai daxin ji cewa sun kasance, suna hana mutane sauraron manzon Allah a yayin da yake karata Kur'ani, domin kada ya yi musu tasiri. An ruwato cewa Xufail xan Umar da Addausi mawaqi sun zo Makka sai wasu Quraishawa suka gargaxe su da cewa: Kada su sake su saurari manzon Allah (s.a.w), suka yi ta tsorata su har sai da suka saka auduga a kunne wai don kada su ji abin da manzon Allah (s.a.w) yake cewa, amma daga baya sai ya yi nadama, ya je ya saurare shi yana karatun Kur'ani mai girma, sai ya ji daxi, ya yi mamaki, a qarshe ya bi manzon Allah har cikin gidansa.

Ya ce: Ya Muhammad, haqiqa mutanenka ba su gushe ba suna cewa kaza da kaza, suna kuma tsoratar da ni a kan al'amarinka, har sai da na toshe kunnena da auduga don kada na ji maganarka, amma Allah (s.w.t) bai yarda ba, har sai da na ji maganarka, na kuma ji ta mafi daxin

(1) Manmu'ul Bayan: j10/584.

zance, saboda haka yanzu ka faxa mini al'amarinka.

Sai manzon Allah (s.a.w) ya bijiro masa da kalmar shahada, ya kuma karanta masa Kur'ani. Sai yake cewa: Wallahi ban tava jin magana mai daxin wannan ba, ban tava ganin adalci irin wannan ba. Daga nan na musulunta na karvi shahada ta gaskiya[1].

2- Labarin Gaibi A Cikin Kur'ani:- Kur'ani ya bayar da labaran gaibi masu yawa, waxanda aka tabbatar da su daga baya. Daga cikinsu akwai: Yayin da manzon Allah (s.a.w) yake Makka, Farisawa sun yi galaba kan Rumawa a yayin yaqi a tsakanin daulolin biyu, a wancan lokaci, Quraishawa sun yi farin ciki da wannan nasarar musulmai kuma sun yi baqin ciki. Domin Rumawa sun fi kusa da Musulmi, tun da dama su kiristoci ne, kuma sun yi imani da Annabi Isa (a.s), sai ga aya ta sauka tana cewa: **Alif lam mim, an yi nasara a kan rumawa a cen qarshen qasa (qasa mai nisa) sai dai bayan galabar da a ka yi a kansu, da sannu su ma za su yi nasara. A cikin 'yan shekaru kaxan. Lallai al'amarin na Allah ne, gaba da baya, a wannan lokacin muminai ma za su kasance cikin farin ciki da**

(1) Albidaya wannihaya, na ibni kasir: j3/123).

**nasarar ubangiji, shi ke ba da nasara ga wanda ya so, domin shi mabuwayi ne, mai rahama, alqawarin Allah ne! Allah ba ya sava alqawarinsa, sai dai mafi yawancin mutane ba su san haka ba.** Suratur Rum: 1-6.

Kuma haka ya kasance dukkanin waxannan sun tabbata, tun da Rumawa su ma sun yi nasara a kan farisawa, a wani yaqin da aka yi cikin wasu shekaru kaxan da ba su kai goma ba,-sai ya haxu da farin cikin muminai a daidai wannan lokacin, saboda nasarar da Allah (s.w.t) ya bayar a kan mushirikai a yaqin Badar mai girma.

**3- Shari'a Tatacciya**

Shari'a tatacciya wacce ta tattara dukkanin vangarorin rayuwa: Shari'a ta tattaro dukkanin rayuwar xan Adam a matsayinsa na shi kaxai da kuma al'umma baki xaya, na daga ibadu waxanda suka kyautata alaqar mutum da Ubangijinsa. Kama daga abin da ya faru na daga tsarkake zuciya da tsarin rayuwar iyali da al'umma baki xaya. Kana ba zai yiwu ba a ce mutumin da ya qirqiri wannan ya zama wanda ya rayu kafin qarni na goma sha huxu (14) ne, da ya ta so a cikin al'ummar da ke cike da rarraba da kuma jahilci.

Haqiqa da yawa daga cikin masu bincike da tunani daga turawan yamma, sun faxaka da irin wannan, sai wannan ya zama shi ne babban dalilin da ya sa musulunci yake samun qarvuwa.

Zamu isu da waxannan 'yan dalilan da ke nuna gajiyarwar Kur'ani, mai buqatar qarin bayani, sai ya koma ga manya-manyan littattafai.[1]

---

(1) A koma zuwa ulumul qur'an dursun manhajiyya, na mawallafin wannan littafin; 14.

## Annabi Muhammad (s.a.w) Makka Abar Girmamawa

An haifi Annabi Muhammad xan Abdullahi (a.s) sha bakwai ga watan Rabi'in auwal, shekara ta hamsin da bakwai bayan haihuwar Annabi Isa (a.s), ana kiran wannan shekara da shekarar giwa.

Sunan mahaifinsa Abdullahi, xan Abdul Muxallabi xan Hashim, kuma ya kasance a cikin mahaifiyarsa lokacin da mahaifinsa ya rasu.

Sunan mahaifiyarsa Aminatu 'yar wahabi, ta rasu ta bar manzon Allah (s.a.w) yana xan shekara shida lokacin da kakansa Abdul muxallabi ya rasu manzon Allah (s.a.w) yana xan shekara takwas. Daga nan sai qanin mahaifinsa ya ci gaba da kula da shi. Manzon Allah (s.a.w) ya auri nana Khadija yana xan shekara ashirn da biyar.

Haqiqa manzon Allah (s.a.w) ya qaurace wa bautar gumaka da mutanensa suke yi don ya kasance mai imani da Allah shi kaxai ba shi da abokin tarayya. Yana tafiya wani kogo da ake kira kogon Hira a can bayan Makka don bautar Allah (s.w.t).

Yayin da ya kai shekara arba'in, sai Allah (s.w.t) ya zave shi da annabta, ayoyin Kur'ani suka fara

sauka a gare shi. An ruwaito cewa, farkon abin da aka fara saukar masa ita ce, faxin Allah (s.w.t):

**Ka yi karatu da sunan ubangijinka, wanda ya halitta. Ya halicci xan Adam daga gudan jini, ka yi karatu da sunan ubangijinka mafi girma, wanda ya sanar ta hanyar alqalami, ya kuma sanar da mutum abin da bai sani ba**. Suratul Qalam:1-5.

Imam Ali (a.s) ya yi imani da manzon Allah (s.a.w) da saqonsa, haka ma matarsa nana Khadija 'yar Huwailid (a.s). Manzon Allah (s.a.w) ya fara kiran mutane zuwa imani da Allah (s.w.t), a cikin kwanciyar hankali da nutsuwa, sannan aya ta sauka inda Allah (s.w.t) yake cewa: Ka yi gargaxi ga 'yan uwanka na kusa. Suratus Shu'ara:214.

Ya kira 'yan uwansa na kusa da su yi imani da saqon Musulunci, sai Allah (s.w.t) ya saukar da: Ka isar da abin da aka umarce ka, kana ka kawar da kai daga mushirikai. Suratul Hijr: 94.

Sai manzon Allah (s.a.w) ya hau kan dutsen Safa a cikin Makka ya kira mutane da su yi imani da addinin musulunci amma suka qi, suka kuma dage a kan bautar gumaka da tsananta cutar da manzon Allah (s.a.w) da sahabbansa da kuma azabtar da su, har wasu suka yi hijira zuwa Habasha. Daga baya sai Allah (s.w.t) ya umarci Annabinsa da ya yi hijira zuwa Madina abar

haskakawa, wacce ake kira (Yasrib). Bayan wasu daga mutanen Madina sun yi masa mubaya'a da alqawarin za su ba shi kariya da sauransu Musulmi.

Bayan shekara sha uku (13) da ya yi a Makka (s.a.w), sai ya yi qaura zuwa Madina domin ya tabbatar da daular Musulunci a can, amma duk da haka mushirikai ba su saurara da qiyayyar da suke masa ba, har suka haxa runduna ta yaqi tare da yahudawa, a kan cewa sai sun qawar da manzon Allah (s.a.w) da Musulunci. Nan fa musulmai suka yi ta kara wa da su a yaqoqi daban daban domin kare addininsu da kuma kawunansu.

Muhimman yaqoqin da suka yi sun qunshi: Yaqin Badar da yaqin Uhdu da yaqin Khandaq da kuma yaqin Khaibar. Kai har dai aka sami yanayin da aka yi Fatahu Makka (buxe Makka). Manzon Allah (s.a.w) ya shiga Makka tare da rundunar Musulmi masu yawa a shekara ta takwas bayan hijira.

Bayan nan manzon Allah (s.a.w) ya yi rashin lafiya mai tsanani, har ya koma ga mahaliccinsa Allah (s.w.t) a cikin shekara ta goma sha xaya bayan hijira, sai musulmi su ka shiga cika baqin ciki da damuwa, tsira da aminci ya tabbata a gare ka da alayenka tsarkaka ya ma'aikin Allah, ya kuma saka maka da alheri game da al'ummarka (s.a.w).

**Tambayoyi**

1- Faxi dalilai guda biyu da suke tabbatar da samuwar Allah (s.w.t).

2- Da me za ka qarfafa dalili a kan kore shirka ga Allah (s.w.t)?

3- Ta yaya za ka tsarkake Allah (s.w.t) daga barin zalunci?

4- Su waye Ulul Azmi a cikin annabawa?

5- Kawo siffofin Annabi.

6- Me ake nufi da Isma?

7- Mece ce mu'ujizar Annabi Musa (a.s) da mu'ujizar Annabi Isa (a.s)?

8- Kawo Vangarori biyu na gajiyarwar Kur'ani?.

9- A wace shekara aka haifi Annabi Muhammad, kana a wace shekara ya rasu?

10- Wane ne ya ci gaba da kula da rainon manzon Allah (s.a.w) bayan rasuwar kakansa Abdul Muxallabi?

## Darasi Na Shida

### Ginshiqi Na Huxu: Imamanci

Imamanci shi ne wakiltar Annabi a kan al'amuran addini da na duniyarsa bayan ya koma ga mahaliccinsa (s.a.w), kuma dole wannan imami ya kasance Annabi ne zai ayyana shi, domin shi ne ya fi kowa sanin wanda ya fi cancantar wanda zai iya xaukar wannan nauyi. Shi ya sa kowane Annabi daga cikin annabawan da suka gabata shi yake ayyana khalifansa da kansa.

Misali: Annabi Musa (a.s) ya ayyana Yusha'u xan Nun a matsayin wasiyyinsa. Haka nan Annabi Sulaiman xan Dawud (a.s) shi ya ayyana Asif xan Khayya a matsayin wasiyyinsa. Haka nan Annabi Isa xan Maryam (a.s) ya ayyana Hawariyawa a bayansa.

Farkon aiko Annabi Muhammad (s.a.w) da saqon Musulunci, sai wani daga cikin Banu Amir, sunansa Barhayaa xan Faras ya ce: Shin yaya kake ganin idan muka bi ka a kan al'amarinka, sannan Allah ya ba ka nasara a kan wanda ya sava maka, shin wannan al'amarin zai dawo hannunmu (Suna nufin khalifanci) a bayanka? Sai manzon

Allah (s.a.w) ya ce: Al'amarin na Allah ne, shi yake saka shi a duk inda ya so.[1]

Sannan Annabi Muhammad (s.a.w) tun daga farkon aiko shi yake qarfafa cewa, al'amarin khalifanci na Allah ne, wanda ya ayyana mana khalifofinsa a bayansa, su ne ahalin gidansa, su goma sha biyu (12). Na farkonsu shi ne Imam Ali (a.s) na qarshensu kuma shi ne Imam Muhammad Almahdi xan Hasan Askari (a.s).

(1) Tarikkhu Umam wal muluk:2/84.

## Halifancin Ahlul Baiti (a.s)

## Hadisan Annabi Muhammad (s.a.w) Kan Halifancin Ahalin Gidansa (a.s)

Musulmi da dukkanin savanin mazhabobinsu sun ruwaito cewa, hadisai da yawa da nassosi a kan imamancin ahalin gidansa guda goma sha biyun nan da muka faxa a baya (a.s), za mu kawo waxansu daga cikinsu kamar haka:

1- Hadisin Saqalaini: Shi ne faxin manzon Allah (s.a.w), in da yake cewa: "Na bar muku waxansu abubuwa biyu (2), matuqar kun yi riqo da su ba za ku vata ba a bayana. Xayansu ya fi xaya girma, wato littafin Allah, Miqaqqiyar igiya ce daga sama zuwa qasa. Xayan kuma shi ne 'ya`yan gidana, kuma ba za su tava rabuwa ba har sai sun same ni a tafki, ku kula da yadda zaku kasance garesu a bayana".[1]

2- Hadisin Fafina: Manzon Allah (s.a.w) yana cewa: "Misalin 'yan gidana a cikinku kamar jirgin ruwan Annabi Nuhu ne, duk wanda ya hau shi ya tsira, wanda kuma ya qi hawa ya halaka."[2]

(1) Jami'us Sahih na tirmizi:5/663.
(2) Biharul Anwar:23/105 da Kanzul Ummal:12/94.

3-A wani hadisin, manzon Allah (s.a.w) yana cewa: "Halifofi a bayana guda goma sha biyu ne, kuma dukkaninsu daga Quraishawa suke".[1]

**Halifofin Manzon Allah Goma Sha Biyu**

1- Imam Ali xan Abi Xalibi (a.s)

2- Imam Hasan xan Ali xan Abi Xalibi (a.s)

3- Imam Husain xan Ali xan Abi Xalibi (a.s)

4- Imam Ali xan Husain (Zainun Abidina) (a.s)

5- Imam Muhammad xan Ali (Albaqir) (a.s)

6- Imam Ja'afar xan Muhammad (Assadiq) (a.s)

7- Imam Musa xan Ja'afar (Alkazim) (a.s)

8- Imam Aliyyu xan Musa (Arrida) (a.s)

9- Imam Muhammad xan Ali (Al-hadi) (a.s)

10- Imam Aliyyu xan Muhammad (Al-haxi) (a.s)

11- Imam Hasan xan Ali (Al'Askari ) (a.s)

12- Muhammad xan Al-Hasan (Al-Mahadi), Almuntazar (a.s)

---

(1) Assiraxal Mustaqima:2/100.

Waxannan su ne Khalifofi (imamai) na manzon Allah (s.a.w), guda goma sha biyu (12), wannan ya sa ake kiran mazhabar gaskiya, mazhabar Shi'a Imamiyya Isna Ashariyya.

Duk wanda ba waxannan ba daga cikin maxaukaka, ko salihai da malamai, ko yaya kuwa matsayinsa a wajen Allah (s.w.t), shi ba imami ba ne. Domin yana daga cikin kuskuren da ya yaxu a riqa yin amfani da lafizin (Imam) a riqa kiran su Abbas, da Hamza, da wasu daga cikin dangin Annabi da manyan malamai,-wanda ba imamai ba da wannan kalmar.

Na'am, wani lokaci wasu mutane suna amfani da kalmar Imam a kan wasu malamai, amma ba suna nufin khalifofin ko Imamai ba ne, suna nufin shugaba ko malami mai tantance al'amura, sai wannan yakan sanya wasu neman falala a wajen wasu don ya kare matsayinsa.



Hubbaren Imam Ali (a.s) a Najaf Mai Daraja

## Darasi Na Bakwai

## Kaxan Daga Tarihin Imamai 12

## Imami Na Xaya: Ali Xan Abi Xalib (a.s)

An haifi Imam Ali (a.s) a cikin Ka'aba kafin shekara goma sha biyu (12) da aiko manzon Allah (s.a.w), kamar yadda dukkanin vangarorin Musulmi suka ruwaito.(1)

Ya yi shahada ranar ashirin da xaya (21) ga watan Ramadan, shekara arba'in (40) bayan hijira, a sakamakon saran takobi da wani la'ananne wanda ake kira da Abdurrahman xan Muljam ya yi masa a kansa, yayin da yake sallar Asuba a rana

(1) Ka duba algadir :6/21 da abin da ke bayan sa.

ta 19 ga watan Ramadan, a cikin masallacinsa. Aka binne shi a Najaf maxaukakiya a Iraqi.

Sunan mahaifinsa Abu Xalibi (Imrana), ya zama shugaban Quraishawa bayan rasuwar mahaifinsa Abdul Muxallabi. Ya kula da ma'aikin Allah (s.a.w), ya ba shi kariya daga cutarwar Quraishawa a shekarun farko na aiko shi. Kuma yana daga cikin waxanda aka tsare su tare da manzon Allah a cikin wani waje da ake kira kwarin Abu Xalib domin yana ba da kariya ga Annabi. Abu Xalib ya rasu bayan aiko manzo da shekara goma (10), a wannan shekarar ita ma nana Khadija matar manzo (s.a.w) ta rasu. Manzon Allah ya kira wannan shekarar da shekarar baqin ciki.

An ruwaito daga gare shi cewa: Kuraishawa ba su iya yi mini wani abu da nake qi ba, har sai da Abu Xalibi ya rasu.[1]

Mahaifiyarsa ita ce Faximatu 'yar Asad, ita ce ta riqi manzon Allah (s.a.w) tun yana qarami, lokacin da ya koma gidan qanin mahaifinsa Abu Xalib (r.a). Ta kasance tana matuqar sonsa da kulawa da shi da tausayinsa.

(1) Tarihul umam wal muluk 2/80.

**Misalan Nassosin Imamancin Ali (a.s)**

1 –A farkon aiko manzon Allah (s.a.w), yayin da ayar inzari ta sauka, wato: "**Ka gargaxi 'yan uwanka na kusa**" . Sai manzon Allah (s.a.w) ya tara 'ya'yan Abdul Muxallabi, ya kira su zuwa Musulunci, yana mai cewa:**"Wallahi ban san wani daga cikinku da ya zo wa mutanensa da wani abu fiye da abin da na zo muku da shi ba. haqiqa na zo muku da alherin duniya da lahira, haqiqa Allah (s.w.t) ya umarce ni da na kira ku zuwa gare shi, wane ne a cikinku zai kasance tare da ni a cikin wannan al'amarin? ya kuma kasance xan uwana, wasiyyina, kuma halifana a cikinku?. Yayin da kowa ya yi shiru, sai Ali (a.s) ya ce: Ni zan zama wazirinka a kan wannan ya ma'aikin Allah! sai manzon Allah ya ce: Wannan shi ne xan uwana, wasiyyina, kuma halifana a cikinku, ku ji daga gare shi, kuma ku bi.**[1]

Sai wasu daga cikin mutanen suka tashi suna yi wa Abi Xalin dariya, suna ce masa: An umarce ka da ka bi xanka, ka ji daga gare shi.

2 – Hadisin Gadir: A taqaice yayin da manzon Allah (s.a.w) zai dawo daga hajjin Ban-kwana, a shekara ta 10, bayan hijira daga Makka zuwa Madina abar haskakawa. Sai mala'ika Jibril (a.s) ya sauka da ayyana Imam Ali (a.s) a matsayin

(1) Tarihul umam wal muluk 2/63.

khalifan manzon Allah (s.a.w) ga Musulmi a bayansa. Allah (s.w.t) yana faxa a cikin Kur'ani mai girma: "**Ya kai wannan manzo, ka isar da abin da aka saukar gareka daga wajen ubangijinka, idan ba ka isar ba to ba ka isar da duk saqonsa ba, kuma Allah ne zai kare ka daga mutane**. Suratul Ma'ida:67.

A nan wurin manzon Allah (s.a.w) ya yi wa Musulmi huxuba, ya ce: "**Ya ku mutane, na bar muku abubuwa biyu, matuqar kun bi su ba zaku vata ba, su ne: littafin Allah da 'ya'yan gidana**[1].

Sannan manzon Allah (s.a.w) yana cewa: Shin ba ni ne na fi cancanta ga kawukanku ba? Suka ce: Haka ne ya Rasulal-Lah!. Ya maimaita hakan har sau uku. Su kuma suna amsa masa da cewa haka ne.

Daga nan sai manzon Allah (s.a.w) ya xaga hannun Imam Ali (a.s) ya ce: Duk wanda na zama shugabansa to Ali ma shugabansa ne". Daga nan sai Annabin rahama ya fara addu'a, yana cewa: Ya Ubangiji Allah, ka jivinci lamarin wanda ya jinvinci lamarinsa, ka yi gaba da duk wanda ya yi gaba da shi. Ka so wanda ya so shi, ka kuma qi duk wanda ya qi shi. Ka taimaki wanda duk ya

(1) Koma algadir 1/31, an cirato daga almustadrak alal sahihain.

taimake shi, ka kuma juya gaskiya tare da shi duk inda ya juya.[1]

Abu Sa'idul Hudri ya ce: Mutane ba su bar wurin ba har sai da wannan ayar ta sauka. Allah (s.w.t) ya ce: "**A yau ne na cika muku addininku, na kuma cika muku ni'imata, sananan na yardar muku da addinin musulunci a matsayin addini**". (Suratul Ma'ida:3).

Hassanu xan Sabitu ya ce: Ya ma'aikin Allah, ka yi mini izinin na yi wasu 'yan baituttuka a kan Ali xan Abi Xalib ka ji su. Sai manzon Allah ya ce: Na yi maka izini da albarkar Ubangiji. Sai Hassanu ya fara baituka kamar haka:

*Ubangijinsu yana kiransa a ranar Gadir,

Awani wuri da ake kira Khum ku saurare shi

*Yana cewa waye shugabanku da majivincin cikinku,

Babu wani voye-vye suka ce

*Ubangijinka shi ne shugabanmu, majivincin lamarinmu,

Kuma babu wanda zai sava wa wannan wulayar

(1) Sawa'iqul muhriqa: 24, an cirato daga turmuzi da nisa'I da ahmad.

*Sai ya ce: Tashi ya kai Ali cewa lallai,

Na yarda ka kasance Imami mai shiryarwa a bayana

*To duk wanda na kasance shugabansa, to wnnan Alin shi ma shugabansa ne,

Ku kasance a gare shi mataimaka masu gaskiya

*Daga nan sai ya yi addu'a, Allah ka jivinci wanda ya jivince shi,

Ka yi gaba da wanda ya yi gaba da shi[1]

A lokacin ne Abubakar da Umar suka ce wa Ali xan Abi Xalib (a.s): Daga yau ka kasance shugaban dukkanin muminai maza da mata.

An tambayi Umar xan Khaxxab, cewa an ga kana aikata wasu abubuwa ga Imam Ali xan Abi Xalib (a.s), kuma ba ka aikata irin wannan ga kowa daga cikin sahabbai. Sai ya ce haqiqa shi shugabana ne.[2]

Daga cikin hadisan Imam Ali (a.s): Mutane sun kasu kaso uku (3): Akwai malamai masana Ubangiji, da mai neman sani bisa tafarkin tsira, da kuma gungun taci-barkatai, mabiya duk wani mai haniniya, masu bin hanyar da iska ta ke yi,

(1) Algadir an cirato daga hafiz isfahani,
2 sawa'iqul muhriaqa 44, daga darul quxni.

waxanda ba su tsarkaka ba da hasken ilimi, kuma ba su dogara da ingantaccan tutse ba.

Yana daga cikin abin da aka ruwaito a kan amsar addu'arsa (a.s), cewa Mu'awiya xan Abi Sufyan ya shirya runduna a qarqashin wani mutum da ya qware wajen zubar da jinin mutane, ana kiransa Bishr xan Arxat, domin ya keta alfarmar Musulmi da salihai a Yaman. Ya kuma je Yaman don ya halatta jinanensu ya karkarshe mutane da yawa, maza da mata da qananan yara.

Yayin da Imam Ali xan Abi Xalib ya sami labarin abin da wannan la'anannen mutum ya aikata, sai ya yi masa addu'a ya ce: Ya Ubangiji, haqiqa Bishr ya sayar da addininsa da duniyarsa, kada ka kashe shi har sai ka cire masa hankalisa.

Sai Allah (s.w.t) ya amsa addu’ar Imam Ali, domin Bishr ya haukace daga baya, ya kasance yana neman takobi, sai a ba shi takobin itace ya riqa dukan da ita, har sai ya suma, bai gushe ba yana yin haka har ya mutu.(1)

An ruwaito cewa Imam Ali (a.s) ya kira 'ya'yansa Hasan da Husain (a.s) da sauran 'ya'yan gidansa, lokacin rasuwarsa, daga cikin wasiyyar da ya yi musu, ya ce musu:

---

(1) Ka kama kitabul garat :2/140- 142.

Ina yi muku wasici da dukkanin `ya`yana da ahalina da dukkanin wanda wasiyyata ta isa zuwa gare shi, da tsoron Allah, da tsara al'amuranku da kuma sasanta tsakaninku, domin na ji kakanku manzon Allah (s.w.t) yana cewa: Sasanta tsakani ya fi yawan salla da azumi.

Ya ci gaba da cewa: Ina haxa ku da Allah, ina haxa ku da Allah cikin al'amarin marayu, kada ku rufe bakunansu, kada ku tozarta su. Sannan ya sake cewa: Ina haxa ku da Allah, ina haxa ku da Allah dangane da moqotanku, domin su wasiyyar Annabinku ne. bai gushe ba yana wasiyya a gare shi har sai da muka yi zaton cewa za su iya gado.

Ya sake cewa: Ina haxa ku da Allah, ina haxa ku da Allah dangane da salla, domin itace ginshiqin addininku.[1]

(1) Nafahat minal sirah: 60.



Qaburburan Imaman Ahlul-bait (a.s) da suke Baqiyya waxanda wahabiyawa suka rusa su a shekarar 1344 H.

## Imami Na Biyu: Hasan Xan Ali (a.s)

An haife shi a cikin Madina abar haskakawa, a cikin shekara ta uku bayan hijira. Ya yi shahada cikin Madina a shekara ta hamsin (50) bayan hijira. Ya yi shahada ta hanyar shayar da shi guba, wacce Mu'awuya xan Abu Sufyan ya ba wa matarsa mai suna Ja'adatu 'yar Ash'as. An binne shi a maqabartar Baqiyya a Madina abar haskakawa.

Manzon Allah (s.a.w) ya faxa a game da shi da xan uwansa cewa: Hasan da Husain jagorori ne, sun yi jagorancin a zahiri ko kuwa.[1]

(1) Biharul anwar 34/291.

Haka nan ma manzon Allah (s.a.w) ya ce: Hasan da Husain shugabannin samarin aljanna ne.

Jabiru ya ce: Na ji Hasan yana cewa: Kyawawan xabi'u guda goma ne:

"Gaskiyar harshe da Juriya da Haquri a cikn tsanani da Bai wa wanda ya roke ka da Kyakkyawar xabi'a da Ba ya nuna ya fi waninsa da Yana sadar da zumunci da Yana damuwa da al'amarin maqota da Sanin haqqin xan uwansa da Kyautata wa baqo da Mafificin waxannan dukan su ita ce kunya"[1].

Mahaifinsa shi ne Imam Ali xan Abi Xalib (a.s), mahaifiyarsa ita ce Faximatuz Zahra (a.s), ita ce manzo ya faxa a kanta cewa, kamar yadda ya zo a cikin hadisi: "Faxima shugabar matan duniya ce".[2] Kuma "ita ce shugabar matan gidan aljanna".[3]

Ya ci gaba da faxa, wato ya ce: Faxima tsoka ce daga jikina, wanda ya cutar da ita ya cutar da ni, kuma wanda ya so ta ya so ni.[4]

An ruwaito wani mutum daga cikin mutanen Sham, waxanda suka tasirantu ya zama xabi'arsu abin da Mu'awuya xan Abu Sufyanu ya assasa na

(1) Tarihin yaqubi : 2/226.
(2) A koma mishkilil asar: 1/48.
(3) Aljami'ul sahih na buhari: 4/183 da 209 da 219.
(4) Sahihul buhari a cikin littafin fara halitta.

vatunci a kan Imam Ali xan abi Xalib (a.s) da 'ya'yansa. Kamar yadda halin wannan mutumin yake xaya ne daga cikin masu qaramin tunani, ko waxanda aka yaudare su da yaxa jita-jita. Wannan mutum ya ga Imam Hasan (a.s). sai ya fara la'antarsa. Shi kuma Imam ya yi shiru.

Lokacin da wannan mutumin na Sham ya gama, sai Imam Hasan (a.s) ya fuskance shi, ya yi masa sallama, ya yi murmushi ya ce da shi: “Ya kai wannan malami, ina zaton kai baqo ne, da ka tambaye mu wani abu ne da mun ba ka. Ko kana neman shiyarwa ne mu shiryar da kai, kuma idan ka kasance mai jin yinwa ne da mun qosar da kai. Idan ka kasance matsiraici (mara tufa) ne mu tufatar da kai, idan ka kasance mabuqaci za mu wadatar da kai. Idan ka kasance korarre mu ba ka masauki, kuma idan kana da wata buqata za mu biya maka ita”.

Sai wannan mutumin na Sham ya yi mamakin irin waxannan kyawawan xabi'u na Imam Hasan (a.s). Nan da nan sai ta bayyanar masa waxannan labarun da Banu Umayya suke yaxawa a kan Ahlul Baiti (a.s) qarya ne. Sannan ya ce: Na shaida lallai kai halifan Allah ne a bayan qasa, Allah yana sanya saqonsa a inda ya so. A da na kasance a duk cikin halittun Allah babu wanda nake qi kamar kai da mahaifinka, amma a yanzu

kai na fi so a cikin dukkanin halittun Allah (s.w.t).[1]

(1) Manaqibu ali abi xalib: 3/184.



Haramin Imam Husain (a.s) a Karbala Mai Tsarki

## Darasi Na Takwas

## Imami Na Uku: Husain Xan Ali (a.s)

Mahaifiyarsa ita ce 'yar manzon Allah (s.a.w). an haife shi a cikin Madina abar haskakawa, shekara ta huxu bayan hijira, ya yi shahada shi da mutum saba'in da biyu (72) daga sahabbansa da ahalin gidansa a filin Karbala, wanda ya yi daidai da goma ga watan muharram, shekara ta sittin da xaya (61) bayan hijira. An binne shi a Karbala

Ya kasance farkon wacce ta fara yi kururwa da kuka a kan shahadarsa ita ce Ummu Salama matar manzon Allah (s.a.w), saboda manzo ya ba ta wata qasa a cikin gilashi, ya ce da ita lallai Jibiril

ya sanar da ni cewa; al'ummata za ta kashe Husain, sai ya ba ni wannan qasar, sannan ya ce da ni: Idan wannan qasar ta koma jini, to ka sani tabbas an kashe Husain (a.s).

Wannan qasar ta kasance a wajen Ummul muminin Ummu salama (r.a). lokacin da ta ga lokaci ya taho, sai ta ajiye wannan kwalabar da manzon Allah (s.a.w) ya ba ta, duk bayan sa'a xaya sai ta dubi kwalbar nan. A lokacin da ta ga wannan qasar ta zama jini, sai ta yi kururuwa tana cewa: Wayyo Husain! Wayyo xan manzon Allah!

Sai mata suka shiga kuka daga kowace unguwa, har sai da kururuwa da kuka ya cika Madina, kowane vangare kukan da ba a tava jin irinsa ba a Madina.[1]

Daga cikin wasiyyarsa (a.s) da ya yi wa xansa Zainun Abidin (a.s) yana cewa: “Ya kai xana, ka ji tsoron zaluntar wanda ba shi da mataimaki a kanka sai Allah”.[2]

Yana daga cikin abin da aka ruwaito dangane da qasqantar da kai na Imam Husain (a.s) cewa: Wata rana ya wuce wasu talakawa sun shimfixa mayafinsu sun gutsuttsura gurasa, sai suka buqace shi da ya zo ya ci tare da su, sai ya zo ya zauna

---

(1) Tarihul yaqubi: 2/226
(2) Alkafi: 2/231.

suka ci tare. Sai ya ce da su: Lallai Allah ba ya son masu girman kai.

Sannan ya ce da su: Idan na gayyace ku za ku amsa mini? Suka ce: Na'an ya xan manzon Allah. Suka tashi tare da shi har suka je gidansa, ya shirya musu liyafa da abin da yake da shi na daga abinci (a.s)




Qaburburan Imaman Ahlul-bait (a.s) da suke Baqiyya waxanda wahabiyawa suka rusa su a shekarar 1344 H.

## Imami Na Huxu: Aliyyu Xan Husain (a.s)

An haife shi a Madina ranar Juma'a, biyar ga watan sha'aban, shekara ta talatin da takwas bayan hijira. Ya yi shahada a shekara ta casa'in da tara (99) bayan hijira, ta hanyar ba shi guba.

An ce mahaifiyarsa ita ce Shahzanan 'yar Yazdajir sarkin qarshe a daular Farisa.

Ya halarci waqi'ar karbala a lokacin yana da shekaru ashirin (20) da haihuwa. Bayan ya yi yaqi tare da babansa, saboda tsananin rashin lafiyar da yake ciki a wannan lokacin, ya kasance san nan wajen zuhudu da ibada, saboda haka ne ma ake yi masa laqabi da ma'abocin kanta, saboda yawan sujjadarsa, ana ganin alamin kanta a goshinsa.

Bayan ya yi shahada, lokacin da aka zo yi masa wanka an samu shacin buhu a kafaxarsa saboda yawan xaukar buhun abinci da yake yi cikin dare yana kai wa gidajen talakawa.

Daga cikin zantukansa yana cewa: Na hane ka da kasala (lalaci), da raki, domin biyun nan su ne mabuxin dukkan sharri. Idan ka yi kasala za ka kasa sauke nauyin da ya hau kanka, idan ka zama mai yawan qorafi (wato raki) ba za ka iya haquri ko (wanzuwa) ba a kan gaskiya.

Yana daga cikin abin da aka hakaito daga haibar, Imam Aliyyu Zainul Abidina (a.s) da matsayinsa a wurin Musulmi, ya zo lokacin da yake xawafi masu xawafi sun yi yawa, sai Hisham xan Abdul Malik xan qabilar Banu Umayya ya zo yana son ya tava Hajarul Aswad (wato dutsen Hajarul Aswad wanda yake jikin Ka'aba). Sai dai saboda yawan mutane ya kasa zuwa kusa da dutsen, sai ya koma gefe guda ya zauna yana jiran mutane su ragu. Yana nan zaune sai ga Imam Aliyyu Zainul Abidin (a.s), lokacin da ya kusanci dutsen domin ya tava Hajarul Aswad, sai duk mutane suka dare suka buxa masa har ya kai ga dutsen, saboda haibarsa da girman al'amarinsa, har ya shafi dutsen ya sumbace shi. Sai mutanen Hisham da wanda suke tare da shi xan Abdul Malik xin suka kewaye shi, suka tambaye shi, cewa: Wane ne wancan? Wato suna tambayarsa dangane da Imam

Aliyyu Zainul Abidin (a.s). Sai shi Hisham ya ba su amsa da cewa: Ban san shi ba, domin kada mutanen Sham su yi kwaxayin zuwa su ji wani abu daga gare shi. A wannan lokacin mawaqin nan Farazdaq yana wajen, nan take ya ce ni na san shi. Sai mutanen Sham suke ce waye shi ya kai baban Firas?

Sai Farazdaq ya rera waqa nan take ya ce:

Wannan shi ne wanda rairayin Makka ya san takun sa*

Kuma xaki (Ka'aba) ma ta san shi, haka ma mutanen da ke rayuwa a wajen Makka da ma matanen cikin Makka;

Wannan shi ne xan fiyayyen bayin Allah dukkansu*

Wannan shi ne mai tsoron Allah tsarkakke, wankakke, kuma alami; -alamin addini-

Wannan shi ne wanda Ahmad zavavve Allah yake mahaifi a gare shi*

Allah yana yi masa salati mutuqar alqalami yana motsi ko rubutu;

-Har zuwa qarshen baitocin-.

Nan da nan sai Hisham xan Abdul Malik ya yi fushi, ya umarci baradensa su fitar da Farazdaq daga wurin -a ka jefa shi a kurkuku-.




Qaburburan Imaman Ahlul-bait (a.s) da suke Baqiyya waxanda wahabiyawa suka rusa su a shekarar 1344 H.

**Imami Na Biyar: Muhammad Baqir (a.s)**

An haife shi a Madina abar haskakawa, a shekara ta (57) bayan hijira, ya yi shahada a shekara ta (114) Ah, an saka masa guba ne, kuma an binne shi a baqiyya.

An karvo daga sahabi Jabir mutumin Madina ya ce: Lokacin da yake yaro ya ji manzo (s.a.w) ya faxa masa cewa: Ya gaishe masa da Imam Baqir (a.s).

Ya ci gaba da cewa: Na kasance ina zaune a wajen manzon Allah (s.a.w), a gefensa akwai Husain yana wasa. Sai manzon Allah (s.a.w) ya ce: Ya Jabir, wannan zai haifi wani xa sunansa Ali. Idan Alqiyama ta tsaya, mai kira zai yi kira,

ina shugaban masu bauta da ya ke ya tashi, sai wannan xan nasa ya tashi. Sannan wannan xan nasa Ali Zainul Abidina (a.s) zai haifi xa sunansa Muhammad, idan ka riske shi ba ka rasu ba ya Jabir, ka isar mini da gaisuwa ta zuwa gare shi. In ji manzo Allah (s.a.w)".(1)

Ya ce da Jabir: "Za ka yi tsawon rai har sai ka haxu da xana, wanda yake daga Husain, ana kiransa Muhammad, zai tsarge ilimin addinin tsargewa, idan ka haxu da shi ka isar mini da gaisuwa ta zuwa gare shi".(2)

Matuqa tabbas ya yaxa ilimin musulunci, kuma malamai da yawa sun yi almajirci a gabansa.

Daga cikin maganganunsa yana cewa: "Ku faxa wa mutane mafi kyawun abin da kuke so a faxi a kanku. Domin Allah yana qin mai yawan la'ana, mai yawan zage-zage, mai yawan sukan muminai."(3)

An ruwaito daga xansa Imam Ja'afar Assadiq (a.s) ya ce: Na kasance ina shimfixa wa mahaifina shimfixarsa, sai na yi jiransa har sai ya zo, lokacin da ya zo ya kwanta a shimfixarsa sai na tashi na tafi shimfixata. Tabbas wani dare ya yi jinkiri bai zo ba, sai na tafi masallacin manzon Allah (s.a.w)

(1) Sawa'iqul muhriqa: 102.
(2) Warakibtul safina: 550, an cirato shi daga shehul mufid.
(3) Masdarin da ya gabata: 553.

ina neman sa, bayan mutane sun yi barci shi kuma yana gefe a cikin masallaci ya yi sujjada babu kowa a cikin masallacin, sai na ji yana faxin: "Tsarki ya tabbata gare ka ya Allah, kai ne Ubangijina, da gaske babu waninka, na yi sujjada a gare ka ya ubangijina domin bauta maka da kuma raunina, ya Allah ka kare ni daga azabarka ranar da za ka tayar da bayinka…".[1]

(1) Alkafi: 3/323.

## Yadda Ya Himmatu Da Tarbiyyar Malamai

Tabbas ya tarbiyantar da malamai masu yawa a kan tafarkinsa da xabi'arsa, har ma an samo daga Imam Ja'afar Assadiq (a.s) ya ce: "Lallai sahabban babana sun kasance ado ne a gare mu, a raye suke ko bayan wafati".(1)

An ruwaito daga gareshi (a.s) yana yi wa xansa Imam Ja'afar (a.s) wasiyya lokacin da zai yi wafati, da faxinsa: Ya xana ina yi maka wasiyya ta alheri ga sahabbaina.

Sai Imam Ja'afar (a.s) ya amsa masa da cewa: Ya babana zan sanya wa kowanne daga cikinsu ya zauna a cikin birni, ta yadda ba zai buqaci tambayar wani mutum ba.

Abin nufi zai ba su ilimi da fagagensa ko vangarorinsa, ta yadda ba za su tava buqatar su tambayi wani malami daban ba.

---

(1) Siratul a'immatul isna ashara: 2/200.




Qaburburan Imaman Ahlul-bait (a.s) da suke Baqiyya waxanda wahabiyawa suka rusa su a shekarar 1344 H.

## Imami Na Shida: Ja'afar Assadiq (a.s)

An haife shi a shekara ta tamanin (80) bayan hijira, ya yi shahada ta hanyar ba shi guba a shekara ta xari da arba'in da takwas (148) bayan hijira a Madina abar haskakawa. An binne shi a baqiyya.

ya mayar da hankali wajen tarbiyyantar da malamai a cikin vangarorin ilimomi daban-daban na Musulunci da waninsu. Hasan xan Ali Alwasha ya ce: “Na sadu da mutum xari tara a masallacin Kufa, wanda kowannen a cikinsu malami ne,

dukkaninsu suna cewa: Haddasana Ja'afar xan Muhammad (a.s)”.[1]

Daga cikin almajiransa akwai Zurarata xan A'ayun da Muhammad xan muslim Assaqafi, da Jabir xan Hayyan sanannen malamin kimiyyar nan.

Daga cikin gudummawar da ya bayar na yaxa ilimin Musulunci da wayar da duniya da ilimantar da ita ga mabiya Ahlul-Baiti (a.s) wato Shi’a, ana danganta masa mazhabar Shi'a Imamiyya Al-Isna Ashariyya, ana cewa mazhabar Ja'afariyya.

Abu Ja'afar Almansur ya aika wajen Imam Assadiq (a.s) yana tambayarsa cewa: Don me ba kwa zuwa wajenmu kamar yadda sauran mutane suke zuwa?

Sai Imam (a.s) ya amsa masa da cewa: Ba mu da wani abu na duniya da muke jin tsaron ka a kan sa, kuma ba ka da wani abu na lahira da muke neman sa a wajen ka, sannan ba ka cikin wata ni'ima ballantana mu taya ka murna, kuma ba ka cikin wata damuwa ko musibar da za mu yi maka jaje ko ta’aziyya a kanta, to don me za mu je wurinka?.[2]

(1) Rijalun najashi: 40.
(2) Warakibtul safina: 562.

Daga cikin maganganunsa (a.s): Duk wanda ya bai wa azzalumi uzuri a kan zaluncinsa, Alllah zai haxa shi da wanda zai zalunce shi. Kuma idan ya yi addu'a ba za a amsa masa ba, kuma Allah ba zai ba shi sakamako a kan zaluntarsa da a ka yi ba.

An samo daga Zakariyya xan Ibrahim ya ce: Na kasance Banasare, sai na Musulunta. Na yi aikin Hajji, na shiga wajen Imam Ja'afar Assadiq (a.s), sai Imam ya ce: Da ni lallai Allah ya shirye ka, tambaye ni ya kai xa na. Sai na ce da shi: Lallai babana da mahaifiyata nasarawa ne, kuma mahaifiyata ba ta gani sosai. sai Imam (a.s) ya ce da shi: Ka kula da mahaifiyarka, ka kasance mai kyautata mata, ka xauki nauyin yi mata hidima. Sai Zakariyya ya ce: Lokacin da na koma Kufa, na kasance mai tausayi ga mahaifiyata da yi mata hidima. Sai ta ce da ni: Ya xana, a da, ba ka yi mini abin da kake yi mini a yanzu, alhali da kana kan addinina, mene ne ya canza ka haka, bayan shigarka addinin Musulunci?

Sai na ce: Wani mutumne daga cikin 'ya'yan Annabi ya umarce ni da hakan. Sai ta ce: Ya xana addininka shi ne mafificin addini, faxa mini yaya yake. Sai na sanar da ita ginshiqan Musulunci da vangarorin koyarwarsa. Sai ta musulunta ta yi

salla. Bayan haka sai ta rasu, Allah ya gafarta mata.[1]

(1) Al-ihtisas: 190.



Hubbaren Imam Kazim da Jawad (a.s) da aka fi sani da Kazimiyyain

## Darasi Na Tara

## Imami Na Bakwai: Musa Alkazim (a.s)

An haife shi ashekara ta xari da ashirin da takwas (128) bayan hijira, ya yi shahada ta hanyar ba shi guba a cikin kurkukun Harunar Rashid, a shekara ta xari (183) bayan hijira. An binne shi a cikin Bagadaza (babban birnin Iraqi) a wani yankin daga cikinta, da aka fi sani da birnin Kazimiyya.

Ana yi masa laqabi Kazim ne saboda kowa ya san shi wajen haquri da kamewa a kan fushi. Ya fuskanci abubuwa masu yawa masu tsanani daga mahukuntan zamaninsa musamman Harunar

Rashid, wanda ya sha sanyawa a kama shi a mafi yawan lokuta. Ya ci gaba da kama shi yana tsarewa, karo da dama, tsawon shekaru, wanda kowane kamu ya sava wa wanda ya gabace shi ta vangaen yanayin tsoratarwa da takurawa.

Muhammad xan Xalhat mai bin mazhabar Shafi'iyya ya ce: "Shi imami ne mai girman al'amari, mai girma ne, mai qoqari, sananne ne a ibada, mai dauriya wajen bin Allah, sananne wajen karamci, yana kwana yana mai yin salla, yana mai yawaita yin sadaka, da rana yana yini azumi, mai juriya ga duk wanda ya yi masa kuskure, ya kawar da kai da afuwa ga wanda ya yi masa wauta. Don haka a kan kira shi Kazim (mai kamewa".[1]

Daga cikin wasiyyarsa ga Hisham xan Hakim: Lallai Allah yana da hujjoji biyu a kan mutane. Hujja bayyananniya da hujja voyayya. Hujja bayyananniya ita ce manzanninsa da annabawa da imaman Ahlul-Baiti (a.s). hujja ta voye ita ce: Hankulanku ya kai Hisham. Aiki kaxan da mai hankali ya yi karvavve ne kuma abin ruvanyawa. Aiki da yawa na masu jahilci abin mayarwa ne ba a karva.

An hakaito Imam Musa Alkazim (a.s) yana tafiya a kan hanya, sai ya wuce wani babban gida

(1) Warakibtus safina 565, daga maxalibil su'al: 18.

na xaya daga cikin mawadata, sai ya ji waqa da kaxe-kaxe suna tashi daga cikin kowane gida. Sai ga 'yar wanke-wanken gidan ta fito domin ta zubar da ragowar abinci a kan gefen hanya. Sai Imam (a.s) ya masta kusa da ita ya tambaye ta, ya ce: Wannan gidan waye? sai ta ce gidan shugabana Bishir ne.

Sai Imam ya ce da ita: Wannan shugaban naki bawa ne ko xa? Nan da nan sai ta ce: Xa ne. Sai Imam (a.s) ya ce: Haka ne, domin da bawa ne da ya yi biyayya ga shugabansa, (ma'ana da ya san shi bawan Allah Maxaukaki ne da ya bi shi ya bar shan giya da yin kaxe-kaxe waxanda aka haramta).

Sai ta shiga gida lokacin da Bishir ya fahimci ta xan yi jinkirin dawowa, sai ya tambaye ta, meye ya tsayar da ita? Sai ta ba shi labarin abin da ya gudana tsakaninta da Imam (a.s) na maganganun da ya yi mata. Sai waxannan maganganun da Imam ya yi suka yi tasiri a zuciyar Bishir, sai ya xauki kofin giyar da ke hannunsa ya jefar da shi, ya biyo Imam kazim (a.s) da gudu, a qafarsa ko takalmi ba bu. Yayin da Imam ya gan shi, sai ya gane shi, sai ya tuba a hannunsa, daga nan ya zama cikin masu bautar Allah da gudun duniya, har ya shahara aka san shi da Bishir mai yawo babu takalmi (alhafi).



Hubbaren Imam Ridha (a.s) a Mash'had (Khurasan)

**Imami Na Takwas: Aliyyu Arrida (a.s)**

An haife shi a shekara ta xari da arba'in da takwas (148) bayan hijira, ya yi shahada ta hanyar ba shi guba a shekara ta (203) AH. An binne shi a Madina. Dukkanin al'ummar Musulmi sun san shi da karamci da hikima, har sai da Ma'amun Al'abbasi ya buqace shi da ya zama wazirinsa, ya karva saboda takurawar Ma'amun da abubuwan da ya tanada zai yi wa Imam da mabiyansa na cin zarafi.

Amma duk da haka sai Imam ya saka masa sharaxin ba zai xauki ko wace irin doka ko wani abu na hukuma a hannunsa ba.

Imam (a.s) ya tsaya kai da fata, wajen yin raddi ga zindiqai da karkatattun mutane, haqiqa manya manyan litattafai cike suke da tattaunawarsa tare da su, har sai da fificinsa ya yaxu a duniya a tsakanin maqiyansa da abokan husuma ko karawarsa, ballantana kuma masoyansa.

Yana daga cikin zantuwarsa (a.s): Abokin kowane mutum shi ne hankalinsa, maqiyinsa kuwa jahilcinsa. Tsafta tana daga cikin xabi'ar annabawa.

An samo cewa Abunu'as mawaqi ya koka da rashin yi wa Imam waqa, sai ya yi wasu 'yan baitoci ga Imam (a.s), ya ce:

An faxa mini cewa: kai ne ka fi dukkan mutane ilimi*

A dukkan vangarori na zance mai faxakarwa;

Ka cancanci yabo saboda kyakyawan tunaninka*

Tamkar `ya`yan itaciyar zinare a hannun matsinka kayan marmari;

Don me ba ka yi baitocin yabo ga xan Musa ba*

Tare da duk waxannan siffofin -na alkhari- da ya tara;

Sai na ce: matsayi na bai kai in zama mai yabon imamin da*

Jibirili ya kasance hadimin babansa ba;

An ruwaito cewa lallai Abumansur xan Abdurrazaq ya ce da sarkin birnin Xus in da aka binne Imam Ridha (a.s), a wannan lokacin kiran ta (Xus), shin kana da xa kuwa? Sai sarkin ya ce: A'a.

Sai Abumansur ya ce: don me ba za ka je kabarin Imam Ridha ba ka roqi Allah ya azurtaka da xa ba, domin ni na roqi Allah buqatuna ya biya mini.

Sai sarkin ya ce: Sai na je kabarin Imam (a.s) in da yake kwance, na roqi Allah a wajen Imam Ridha domin ya azurta ni da xa. Sai Allah mai girma da buwaya ya azurta ni da xa namiji.[1]

Allah ka azurta mu da ziyartar Imam Ali Ridha xan Musa a nan duniya, da cetonsa da na iyayensa, da na kakansa (s.a.w) a lahira.

Daga cikin abin da aka ruwaito cewa: Wani mutum sunansa Sulaiman xan Ja'afar Alja'afari ya ce: Na kasance wata rana a wajen Imam Rida (a.s), a gaban sa akwai kwatarniyar abinci. Sai ya ga wani mutum da sauri, sai ya xauke hannunsa daga kan abincin, sai mutumin ya qaraso ya ce da Imam: Yanzun nan Zubairu ya mutu, ya kasance azzalumin sarki. Sai Imam Ridha (a.s) ya xaga

(1) Isbatul hudatu: 3/285.

kansa ya ce: Lalle ina tsammanin ya aikata babban zunubi a cikin wannan daren, Allah maxaukakin sarki ya ce: "**Sakamakon zunuban da suka aikata ne, aka dulmiyar da su kuma aka shigar da su wuta**".[1]

Sannan ya mayar da hannunsa kan abincin, sai wani yaro ya zo ya ba shi labarin mutuwar Zubair, ta dalilin shan giya da kuma wuce iyaka a cikin shanta a cikin daren da ya wuce.

(1) Surar Nuhu: 25.



Hubbaren Imam Kazim da Jawad (a.s) da aka fi sani da Kazimiyyain

**Imami Na Tara: Muhammad Aljawad (a.s)**

An haife shi a shekara ta xari da casa’in da biyar (195) bayan hijira, ya yi shahada ta dalilin ba shi guba da umarnin Mu'utasim Al'Abbasi, shekara ta xari biyu da ashirin (220) bayan hijira. An binne shi a birnin Kazimiyya.

Duk da qarancin shekarunsa ya shahara da ilimi da falala. Ma’amun ya aura masa 'yarsa mai suna Ummu Fadl. Idan za mu yi magana a kan Imam da iliminsa, duka lokacin da mahaifinsa ya yi wafati shakarunsa ba su kai goma ba, kuma bai sami iliminsa ba ta hanyar wasu malamai na daban ba, wannan zai bayyana maka imaman

Ahlul-Baiti (a.s), iliminsu da falalarsu da kuma taqawarsu daga waninsu.

Daga cikin zantukansa (a.s): Da jahili zai yi shiru da mutane ba su samu savani ba. Ya ci gaba da cewa: Shi mumini yana buqatar dace a wajen Allah da kuma mai yi masa wa'azi, da karvar nasihar duk wanda ya yi masa nasiha.

An sami daga xaya daga cikin masu karvo hadisi, sunansa Ahmad xan Hasan ya ce: Na kasance wata rana ina zaune a wajen Ali xan Ja'afar (a.s), -baffan Imam Ridha (a.s) a masallacin manzo (s.a.w) abar haskakawa. Ya kasance ya tsufa sosai kuma na kasance ina amfana daga iliminsa. Lokacin da Imam Muhammad Jawad ya shiga, sai Ali xan Imam Ja'afar Assadiq ya yi sauri ya tare shi ba tare da ya saka takalminsa ko abayarsa ba. Ya sumbace shi ya girmama shi, sai Imam Jawad (a.s) ya ce da shi: Zauna ya kai qanin mahaifina (ammina). Sai ya ce: Ya shugabana yaya zan zauna alhali kai kana tsaye? Bayan an tashi daga zaman majalisin, sai Aliyyu xan Ja'afar ya dawo majalisin karantarwarsa. Sai wasu daga cikin xalibansa suka zarge shi, suka ce da shi: Kai qanin mahaifinsa ne amma ta yaya kake ba shi irin wannan girma?!

Sai ya ce da su: Ku yi shiru, idan har Allah mai girma da buwaya bai kasance ya sanya wannan furfurar- Ya riqe gemunsa- ahalin imamanci ba?

kuma ya sanya wannan saurayin ahalinta. Ta yaya kuwa zan iya musa fificinsa?!. Muna neman tsarin Allah daga abin da kuka faxi.[1]

An ruwaito cewa Imam Jawad (a.s), lokacin da ya yi niyyar barin Bagdad zai koma Madina abar haskakawa, ya isa har titin da zai kai ga qofar shiga Kufa, sai ya shiga wani masallaci domin ya yi salla, ya kasance a kewaye da masallacin akwai wata bishiya ba ta yin 'ya'ya. Sai Imam ya yi alwala a gindin wannann bishiyar. Ya yi sallar magariba a jam'i, sai ya miqe ya kawo raka'a huxu nafilar bayan magariba. Bayan ya gama addu'o'in bayan salla, ya yi sujjadar godiya ga Allah. Sai mutane suka ga bishiyar nan ta magarya ta yi 'ya'ya, suka yi mamaki a kan hakan, har suka ci 'ya'yanta, sai suka same su nunannu, masu zaqi, kuma ba qwallo a cikin su.[2]

(1) Alkafi: 1/223.
(2) Ka koma izuwa kitabul irshad: 2/288.



Qubbar Imam Ali Askari da Imam Hasan Askari (a.s) da aka fi sani da Askariyyain



Cikin Hubbaren Askariyyain a Birnin Samarra' kafin 'yan ta'adda su sanya masa Bom



Hubbaren Askariyyain a Birnin Samarra' bayan 'yan ta'adda sun sanya masa Bom

**Imami Na Goma: Aliyyu Alhadi (a.s)**

An haife shi a shekara ta xari biyu da sha biyu (212) bayan hijira, ya yi shahada ta hanyar ba shi guba a garin Samra'a a shekara ta xari biyu da hamsin da huxu (254) bayan hijira. An binne shi a cikinta.

Lokacinsa ya yi kama da na Imam Alhadi (a.s) ta vangaren cutarwa da hana walwala daga vanaren hukuma, musamman a zamanin Mutawakkil Al'Abbasi, wanda ya kasance mai tsananin qiyayya a kan zuriyar Ali xan Abi Xalib (a.s), shi ne wanda ya yi umarni a rusa hubbaren

kabarin Imam Husain (a.s), a kuma xaure duk wanda ya ziyarce shi.

Mutawakkil ya aika Yahaya xan Arsamata domin ya taho da Imam (a.s) daga Madina zuwa Iraq. Yahaya ya ce: Sai na tafi Madina, lokacin da na shiga, mutanen Madina sun yi kururuwa kururuwa mai tsanani, wacce mutane ba su tava jin irinta ba, saboda jimantawa jin tsaron mai zai sami Ali Alhadi (a.s), in hankula su yi dubu sun tashi, saboda shi ya kasance mai kyautata musu, mai yawan lazimtar masallaci, babu karkata zuwa duniya ko yaya a tare da shi.

Sai Yahaya ya ce: "Sai na riqa rarrasar su ina yi musu rantsuwa da cewa ba a umarce ni da wani mummunan umarni a kansa ba, kuma ba shi da wani laifi, kuma da na bincike gidansa ban sami komai ba, sai Kur'ani da littattafan addu'o'i da littattafan ilimi, sai wannan ya sa ya yi qima a idona..".[1]

Daga cikin maganganunsa (a.s): Duk wanda ya wulaqantar da kansa to ba a aminta daga sharrinsa.

An ruwaito wani mutum sunansa Abdurrahman yana tsaye a qofar Mutawakkil Al-Abbasi. A lokacin da Imam (a.s) ya gabato, sai Abdurrahman

(1) Warakibtus safina: 582.

ya kalli halin da Imam (a.s) yake ciki, sai ya xaga hannayensa yana addu'a ga Imam, shi kuma Imam yana kallonsa. Lokacin da Imam ya zo kusa da shi, sai ya waiga ya ce da shi, Allah ya amsa maka addu'arka ya kuma tsawaita rayuwarka, ya yawaita dukiyarka da 'ya'yanka. Sai haibar Imam ta cika masa ido.

Abdurrahman ya ce sai Allah ya buxe mini alheri da addu'arsa, har sai da dukiyarsa ta yawaita, ya haifi 'ya'ya goma, rayuwarsa ta yi tsawo, ya kasance yana daga cikin waxanda suka yi imani da imamamanci Imam Alhadi (a.s).[1]

A ranar Laraba ashirin da uku (23) ga watan muharram, hijira ta (1427), Sai maqiya `yan ta'adda daga mabiya xawagitai da azzalumai masu kafirta mutane suka sa bom a qaburburan imaman biyu (Ali Alhadi da Hasan Al'Askari, ana kiran su da (al'askariyyaini) wato waxanda qabarin su yake a Askar) wanda hakan ya kai ga rusa hubbarorin qaburburan imaman guda biyu, wannan ya faru ne bayan da suka xau tsawon lokaci suna shiri a kan hakan, har dai daga qarshe suka samu damar saxaxawa, suka lavava a daren da ya gabata, suka dasa manyan bamabamai a kaburburan. Inna lillah wa inna ilaihi raju', Babu wani tsimi ko dabara sai a wajen Allah.

(1)Isbatul hudatu: 3/371.



Hubbaren Askariyyain a Birnin Samarra' bayan 'yan ta'adda sun sanya masa Bom

**Imami Na Sha Xaya: Hasan Al'Askari (a.s)**

An haife shi a shekara ta (232) bayan hijira a Samarra’, ya yi shahada a shekara ta (260) bayan hijira, an binne shi a cikinta.

Muhammad xan Abdul'aziz Albalhi ya ce: Wata rana da safe ina zaune a hanyar da dabbobi suke wucewa, can sai ga mahaifina Muhammad yana tahowa daga gidansa, ya nufaci inda mutanen gari suke. Sai na ce a cikin raina, yanzu da zan yi wa mutane shela cewa wannan hujjar Allah ne a kanku, ku bi shi, sai fa su kashe ni?

Lokacin da ya kusanto ni, sai ya yi mini nuni da xan yatsansa da na yi shiru. Sai na gan shi a

wannan daren yana cewa: “Lallai ne ko ka voye ko a kashe ka, ka ji tsoron Allah a kan haka”.(1)

Azzaluman shuwagabanni sun sha kama shi, Mutawakklil Al-Abbasi ya sha saka shi a kurkuku a wajen xaya daga cikin yaransa, ana kiransa da suna Salihu xan Wasif, sai wasu daga cikin Abbasiyyawa suka ce da shi: “Ka quntata masa. Sai salihu ya ce: Ya ya zan yi da shi alhali na wakilta mafi sharrin mutane biyu da ke qarqashina? kan kace me, sai ga su sun yi zurfi a cikin lamarin ibada da salla, sannan ya bayar da umarni da a zo da mutanen guda biyu, sai ya ce musu: Kaicon ku! meye gaminku da wannan mutumin? Sai suka ce da shi: Me za mu ce a kan mutumin da yake azumi da rana yake sallatar dukkan dararensa. Ba ya magana, ba ya shagaltuwa da wani abu in ba ibada ba. Idan ya kalle mu sai gavvanmu su raurawa, mu ji duk mun kasa mallakar kanmu. Da Abbasiyyawa suka ji haka sai suka juya tavavvu, qasqantattu”.(2)

Daga cikin zantukansa (a.s) : Yana daga qanqan da kai, yi wa wanda za ka wuce shi sallama. Da zama a baya-baya ko kuma a abin da bai fi na kowa ba.

(1) Kashful gumma: 3/212.
(2) Ka koma kafi: 1/ 512.

Kuma yana cewa: Taurin kan xa ga mahaifinsa a yayin da yake qarami, zai kai shi ga kangarewa a yayin da ya girma.

Wannan kenan, Imam ya yi shahada a gidansa da ke birnin Samra', kuma an binne shi a can kusa da mahaifinsa (a.s). Qaburburansu sun kasance wajen ziyarar masu ziyara, an adonta ginin da ma hubbaren qabarin da zinare tun tsawon zamani.

A ranar Laraba ashirin da uku (23) ga watan muharram, hijira ta (1427). Sai maqiya `yan ta'adda daga mabiya xawagitai da azzalumai masu kafirta mutane suka sa bom a qaburburan imaman biyu; Ali Alhadi da Hasan Al'Askari, ana kiran su da (Al'askariyyaini) wato waxanda kabarinsu yake a Askar, wanda hakan ya kai ga rusa hubbarorin qaburburan imaman guda biyu, wannan ya faru ne bayan da suka xau tsawon lokaci suna shiri a kan hakan, har dai daga qarshe suka samu damar saxaxawa, suka lavava a daren da ya gabata suka dasa manyan bamabamai a kaburburan. Wannan ya yi daidai da faxin wani mawaqi:

Sun yi baqin cikin da ba su yi tarayya ba*

a kashe shi, sai suka bibiye shi bayan mutuwa

Inna lillahi wa inna ilaihi raju'n, Babu wani tsimi ko dabara sai a wajen Allah!




Darasi Na Goma

**Imami Na Sha Biyu: Muhammad Almahdi (a.s)**

An haife shi a shekara ta (255) bayan hijira, a Samra', kuma yana nan a raye zai bayyana da izinin Allah maxaukaki.

Ibn Hajar ya ce: Shekarunsa a duniya na haihuwa lokacin da mahaifinsa ya yi wafati biyar ne, sai dai Allah ya ba shi hikima. [1]

Lallai hadisai masu yawa sun zo daga manzo (s.a.w) da imamam Ahlul-baiti (a.s) da suke xauke da bayanin bayyanar Imam Mahadi (s.a) da ambatonsa a cikin hadisai.

1- An karvo daga Ali (a.s) ya ce: Manzon Allah (s.a.w) ya ce: Almahdi yana cikin Ahlul-bait, zai bayyana domin gyara.[2]

2- An karvo daga Sa'idu bin Musa bin Musayyib ya ce: Mun kansance muna wajan Ummu Salama tana tunatar da mu Mahadi, ta ce: Na ji manzon Allah (s.a.w) yana cewa: Mahadi yana daga cikin 'ya'yan Faxima (a.s).[3]

3- A cikin hadisin Abdullahi manzon Allah (s.a.w) ya ce: Duniya ba za ta qare ba har sai an sami wani mutum daga cikin Larabawa daga ahalin gidana ('ya'yan gidana) sunansa ya yi daidai da sunana.[4]

4- A cikin wani hadisi an karvo daga manzon Allah (s.a.w) ya ce: Wani mutum zai zo daga

(1) Sawa'iqul muhriqa shafi na (208).
(2) Sannan ibni MajaMujalladi na huxu, shafi xari huxu da hamsin da huxu.
(3) Masdarin da ya gabata.
(4) Sunanu turmuzi: 4/505.

cikin 'ya'yan gidana, sunansa ya yi daidai da sunana.[(1)]

5- Ya zo cikin hadisi daga manzo (s.a.w) ya ce: Da ba abin da ya saura ga tashin duniya sai yini, da sai Allah ya tsawaita wannan yini ya fito da wani mutum daga cikin 'ya'yana, ya cika duniya da adalci, kamar yadda ta cika da zalunci.[(2)]

7- Di'ibil Alhuza'i, a yayin da ya yi wa Imam Ridha wata doguwar waqa wacce aka fi sani da (Xa'iyya), har ya zo zuwa inda yake cewa:

Bayyanar Imam babu makawa zai fito*

Zai tsayu da sunan Allah, da albarkoki;

Zai rarrabe mana qarya da gaskiya*

Zai yi sakamako a kan aikin na gari ko na sharri;

Sai Imam Ridha ya yi kuka sannan ya xaga kansa zuwa gare ni sai ya ce: Kai Bakhuza'e haqiqa amintaccen Ruhi mala'ika Jibril ya yi furuci da wannan baitukan da suka gudana a kan harshenka[(3)].

Haqiqa Allah ya voye Imam Mahadi (a.j) kuma da sannu zai bayyana shi a lokacin da ya dace da hakan da ya tsaya da nauyin da aka xora masa na

(1) Masdarin da ya gabata.
(2) Muhadharat fililahiyyat: 565, daga musnad ahmad bin hambal.
(3) Wa rakibtussafina :590

tsayar da hukuncin Allah Maxaukaki a doron qasa. Wani abin lura shi ne haqiqa ruwayoyin da musulmai suka ruwaito daga manzo suna qunshe da cewa lalle bayyanarsa zata kasance a qarshen zamani, amma ba ta xauke da cewa haihuwarsa zata kasance a wannan lokacin ba, kuma wannan ya yi daidai da ra'ayin da ya tafi a kan voyuwarsa (a.j) kamar yadda Shi'a suka tafi a kai.

**Fatarorin Voyuwa Guda Biyu**

Fatara ta farko: Ana kiran ta gajeriyar fatara, ta fara ne daga shekara ta 330 H. A lokacin da Imam ya zamo yana da xan saqo a tsakaninsa da mutane kuma waxannan 'yan saqon mutum huxu ne dukkaninsu sun rayu a Bagdad kuma a nan aka binne su, kuma qaburburansu sanannu ne, waxannan mutanen su ne:

1- Usman xan Sa'id Al'amuri, wanda da ma ya kasance wakili amintacce a wajen Imam Askari (a.s) ya rasu a shekara ta 280 H.

2- Muhammad xan Usman xan Sa'id Al'amuri ya rasu a shekara ta 304 ko 305 H.

3- Hasan xan Ruh Annubhati, ya rasu a shekara ta 320 H.

4- Aliyyu xan Muhammad Samarri ya rasu a shekara ta 238 ko 329.

Da rasuwar Samarri ne wakilci na musamman ya kawo qarshe, kuma da qarewar wannan fatarar ne, gajeriyar voyuwa ta kawo qarshe, sai kuma

babbar voyuwa ta fara, har zuwa lokacin da Allah zai yi masa izinin bayyana, kuma duk wanda ya yi da'awar wakilci na musamman a lakacin babbar voyuwa to maqaryaci ne maqagin qarya.

A cikin wani hadisi daga Hasan xan Ahmad Mukattab ya ce na kasance a birnin Salam, wato Bagdad, a shekarar da sheikh Abul'hasan Aliyyu Assamarri (Allah ya tsarkake ruhinsa) ya rasu, sai na halarci wajensa kafin wafatinsa da 'yan kwanaki, sai ya fitar wa mutane wata takarda da aka rubuta a cikinta cewa:

**Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jin Qai**

"Ya kai Ali xan Muhammad Assamarri Allah ya girmama ladan 'yan'uwanka a kan rashinka, lalle kai mai mutuwa ne a nan da kwanaki shida, ka tattara lamarinka, kuma kada ka yi wasici ga wani da ya tsaya a matsayarka bayan wafatin ka, haqiqa cikakkiyar voyuwa ta fara, kuma babu bayyana sai bayan da Allah girmansa ya buwaya ya yi izini.

Wannan kuma bayan tsawon zamani mai nisa da qeqashewar zuciya, da kuma cikir doron qasa da zalunci. Kuma da sannu wanda yake da'awar yana haxuwa da ni zai zo wajen Shi'ata, lalle ku kula, duk wanda ya yi da'awar haxuwa kafin fitowar Sufyani da tsawa haqiqa maqaryaci ne maqirqiri. Babu dabara kuma babu qarfi sai daga Allah maxaukaki mai girma.

Ya ce: Sai muka kwafi wannan takardar muka fita daga wajensa, ransa yana kai kawo. Sai aka ce da shi, waye wasiyyinka a bayanka? Sai ya ce: Allah yana da wani al'amari kuma shi zai isar da shi, sannan ya cika. Wannan shi ne qarshen zancen da aka ji daga gare shi, Allah ya qara yarda da shi.(1)

A lokacin voyuwa babba, muminai suna komawa zuwa faqihai da mujtahidai adalai waxanda suka yi fice a fagen sani don sanin hukunce-hukuncensu na addini da kuma shu'unan su na shari'a, gwargwadon yadda ya zo a cikin saqon Imam Mahadi (a.s), yayin da ya zo a cikinsa da faxinsa: Amma fare-faren zamani ku koma zuwa maruwaita hadisanmu, haqiqa su hujjata ce a cikinku kuma ni hujjar Allah ne a kansu.(2)

Kuma yana daga abin da aka naqalto na daga addu'arsa ga muminai:

"Ya Allah na roqe ka da haqqin wanda ya yi gani da kai, kuma da haqqin wanda ya kira sunanka a doron qasa ko a cikin ruwa, ka yi salati a bisa Annabi Muhammad da alayensa, kuma ka wadata ka yalwata wa mabuqata da talakawa daga cikin muminai, kuma ka kawo sauqi da waraka da hutu ga marasa lafiyan muminai, kuma ka aiko da tausayawarka da girmamawarka ga rayayyu daga

---

(1) Biharul anwar: 51/361.
(2) Wasa'ilul shi'a: 18/101.

cikin muminai, ka kuma aika da gafararka ga mamatan muminai, ka kuma mayar da matafiyan muminai zuwa garuruwansu lafiya lau suna masu cin riba da girman Muhammad da alayensa baki xaya”.[1]

A ranar laraba 23 ga muharram 1427, ne ‘yan ta’adda daga cikin rundunar azzalumai masu kafirta mutane suka sa **Bom** a gidan da aka haifi Imam Mahadi wanda kuma a ciki ya voyu daga ganin mutane wanda yake a cikin birnin Samarra’ a Iraqi.

(1) Almisbah: 281/306.

**Ginshiqi Na Biyar: Makoma**

Ma'anarsa shi ne cewa lalle Allah Maxaukaki da sannu zai dawo da rayayyu bayan mutuwarsu a rayuwarsu ta duniya, kuma zai yi musu hisabi a bisa ayyukan da suka yi a cikinta, kuma kowane mutum ya karvi sakamakon aikinsa, wasu a sa su cikin ni'imar aljanna wasu kuma a jefa su cikin azaba.

Haqiqa Kur'ani ya qarfafa, haka ma hadisai, a cikin ayoyi masu yawan gaske a kan cewa a kwai tashi bayan mutuwa kuma akwai hisabi a ranar tashin alqiyama. Allah Maxaukaki ya ce: "**Kuma aka yi busa a cikin qaho sai wanda ya ke cikin sammai ya suma da ma wanda yake doron qasa sai wanda Allah ya so, sannan sai a ka yi wata busar sai ga su a tsaitsaye suna sauraro**". (Suratuz Zumari: 68).

Babu ban mamaki a cikin raya halittu bayan mutuwa, domin haqiqa Allah maxaukaki mai iko ne a kan komai. Kuma ya yi martani ga kafiran nan da suke nisantar yiwuwar hakan, sai ya tuna musu da yadda halitta ta fara, tare da cewa lalle wanda ya halicci xan Adam, da kuma cewa lalle wanda ya halicci xan Adam a farkon farawa zai iya dawo da halittarsa bayan mutuwa: "**Kuma ya buga mana misali sai ya manta da cewa halittarsa aka yi, sannan ya ce waye ke raya matacce bayan da ya zama rududdugaggun**

**qasusuwa* Ka gaya masa wannan da ya qage shi (daga babu) tun daga farko shi ne zai raya shi, kuma shi masani ne a kan kowace halitta**". (Surar Yasin: 78-79).

Ya zama wajibi ga kowane musulmi ya tafiyar da rayuwarsa a kan aikin alheri da kuma bin Allah Maxaukaki, ya kuma nisanci savo da dukkanin abinda bai da ce da sha'aninsa ba, don ya rabauta da yardar Allah Maxaukaki da kuma rahamarsa da ladansa. "Ya ubangijinmu haqiqa mun ji mai kira yana kira zuwa imani yana cewa ku yi imani da ubangijinku sai muka yi imani. "Y**a Ubangijinmu ka gafarta mana zunubanmu kuma ka kankare mana munanan ayyukanmu, kuma ka karve mu tare da bayinka masu biyayya, haqiqa kai ba ka sava alqawari"**. (Suratu Aali Imran: 193-194).

Waxannan su ne tushen aqida, kuma akwai wasu mas'aloli na aqida waxanda aka ambata a manyan littattafai.

Zuwa nan ne wannan tsawaitaccen littafin na Aqida ya kammala, ina roqon Allah Maxaukaki da ya amfanar da `yan'uwa muminai maza da mata da shi musamman ma samarinmu da matasa masu girma, kuma ya karve shi kyakkyawar karva, kuma ya gafarta min zunubaina a ranar sakamako, haqiqa shi ne maxaukaki mafi jinqan masu jin qai.

## Tambayoyi

1- Mene ne Imamanaci?

2- Don me Imam zai zama Annabi ne zai ayyana shi?

3- Ka ambaci hadisai guda biyu a kan imamancin Ahlul-Baiti.

4- Su waye imamai goma sha biyu?

5- Shin Abbas xan Abi Xalib Imami ne?

6- Ka ambaci dalilai guda biyu a kan imamancin Ali xan Abi Xalib.

7- Ka ambaci hadisi a kan Imam Ali xan Abi xalibi.

8- Ka ambaci hadisi daga manzo (s.a.w) a kan imamancin Hasan da Husain.

9- Ka ambaci hadisi a kan kowane xaya daga cikin imamai (a.s).

10- Ka ambaci hadisai uku daga manzon Allah (s.a.w) dangane da imamul Mahadi.

11- Su waye na'iban Imam Mahadi guda huxun nan?

12- Ka ambaci ayar da ta mayar da martini a kan masu musum ranar Alqiyama.

13- Yaushe ne Mujirimai suka rusa kabarin Imam Hasan Askari (a.s)?.

Qarshe watan Rajab 1424 H

Hujjatul Islam Sayyid Riyadh Al-Hakim

Gabatarwa ........................................................................ 6
Darasi Na Xaya .............................................................. 10
Ginshiqan Addinin Musulunci ........................................... 10
Ginshiqi na Farko: Kaxaita Allah ..................................... 10
Mahaliccin Duniya ........................................................ 14
Ginshiqi Na Biyu: Adalci ................................................ 15
Ginshiqi Na Uku: Annabta ............................................... 16
Darasi Na Uku ............................................................... 18
Siffofin Annabi (s.a.w) ................................................... 18
Mu'ujiza ....................................................................... 21
Misalan Mu'ujizozin Annabawa ........................................ 21
Darasi Na Huxu ............................................................. 27
Mu'ujizar Annabi (s.a.w) ................................................. 27
Darasi Na Biyar ............................................................. 33
Kur'ani Mu'ujiza Madawwami ........................................... 33
3- Shari'a Tatacciya ........................................................ 39
Annabi Muhammad (s.a.w) ............................................... 40
Darasi Na Shida ............................................................. 44
Ginshiqi Na Huxu: Imamanci ........................................... 44
Halifancin Ahlul Baiti (a.s) .............................................. 46
Halifofin Manzon Allah Goma Sha Biyu ........................... 47
Darasi Na Bakwai .......................................................... 49
Kaxan Daga Tarihin Imamai 12 ........................................ 49
Imami Na Xaya: Ali Xan Abi Xalib (a.s) ........................... 49
Misalan Nassosin Imamancin Ali (a.s) .............................. 51
Imami Na Biyu: Hasan Xan Ali (a.s) ................................ 57
Darasi Na Takwas .......................................................... 61
Imami Na Uku: Husain Xan Ali (a.s) ................................ 61
Imami Na Huxu: Aliyyu Xan Husain (a.s) ......................... 65
Imami Na Biyar: Muhammad Baqir (a.s) ........................... 69
Imami Na Shida: Ja'afar Assadiq (a.s) .............................. 73
Darasi Na Tara .............................................................. 77
Imami Na Bakwai: Musa Alkazim (a.s) ............................. 77
Imami Na Takwas: Aliyyu Arrida (a.s) .............................. 81
Imami Na Tara: Muhammad Aljawad (a.s) ......................... 85
Imami Na Goma: Aliyyu Alhadi (a.s) ............................... 89

Imami Na Sha Xaya: Hasan Al'Askari (a.s) ........................ 93
Imami Na Sha Biyu: Muhammad Almahdi (a.s) ................ 97
Fatarorin Voyuwa Guda Biyu........................................... 100
Ginshiqi Na Biyar: Makoma............................................. 104